[11/6, 7:22 PM] Oum Hairan&Affan: ME YA JAMIN?

Fauziyya Tasiu Umar
(Oum Hairan)

1-2

Tsugunne a bayan gdan wata matashiyar budurwa ce yar sha shidda zuwa sha bakwai baƙa me matsakaicin tsaho da ɓoyayyen kyau take wankin kayan yara na makaranta tanata rawar sanyi da alamun yanayin hunturun yana kaɗa duk dama Dole ne ya shigeta duba da ko arziƙin rigar sanyi bata samu ba, wani yaro ne qarami da bazai wucce shekara bakwai ba ya fito daga wata ƙofa alamu sun nuna itane ƙofar da zata sadaka da asalin gdan.
Hankalinta nakan wankin da takeyi bata ankare sa tahowar yaron ba saiji tayi ya watsa mata ruwan sanyi a jikinta ta zabura da sauri ta miqe cikin kiɗima take duban yaron idanunta ya kawo ruwa tace "Farook ni ka watsawa ruwa a wannan sanyin ko?" Murgiɗa mata baki yayi yace "an watsa miki ɗin talaka almajira kawai Momy tace kizo ki haɗa mana break in kinƙi kuma ta zaneki"
A sanyaye ta saki aikin da takeyi tana daga rigarta data manne a jikinta ta nufi ƙofar parlourn ta shiga da sallama babu kowa a parlourn sai Muwaddat da jannat ta dubesu dukkansu babu wanda ya samu arziƙin ko wankin idanu ta matsa ta dauki Irfan daketa miƙo mata hannu tana masa murmushi tace "yarinyana ko Pampers baa cire miki ba bari nayi muku wanka sai nabaku abinci Isiya yakaiku makaranta ko?" Ta Faɗi da sigar tambayar yaran Muwaddat ta zunguro baki gaba tace "aa nidai Aunty Anam ki bamu abinci tukunna da yunwa muka tashi"

Saukowar masu gdan ne yasata haɗa nutsuwarta ta durƙusa cikin ladabi tace "barka da fitowa yallabai Hajiya Barka da asuba" baiko kalleta ba yasa kai ya fice a falon Hajiya Salma ce ma ta harareta tace "kinanan kina sakarcin naki na tsiya zaki makarar min da yara ko duba ko Pampers baki cirewa jannat ba saboda ke kin zama mara mutunci to ki makarar dasu sai hankalinki ya kwanta jaka kawai....."
Kalmar ƙarshen ta bugeta sosai ta sunkuyar dakai hakan bai mawa Hajiya Salma ba saida ta saukenta ƙusa a tsakiyar kanta ta rintse idanu hawaye nabin kuncinta inda sabo zuwa yanzu ya kamata ace ta saba da izayar gdannan tunda kusan a cikinta ta rayu tun tana shekara biyar suke tare da mahaifiyarta a wannan gda duk da kasancewar ba'a asalin wannan gidan suke ba mahaifiyarta tana gdansu Aliyu wato mamallakin gdan tanayima iyayensa aiki lkcn da Aliyu yayi aure ne matarsa ta matsa tanason yar aiki shine aka kawo ta gdan nasa matsayin yar aikin

gdan yanzu shekara takwas kenan tana aiki a gdan a gabanta duk aka haifi waɗannan yaran Umar Farooq Muwaddat da jannat amma har yanzu yanci yaqi zuwan mata daga megidan har matar gdan har yaran gdan babu wanda take samun sauqi ta gurinsa har garama Salma wani lkcn takan jata suyi hira idan yan mutumcin na kusa.

Ɗaukar yaran tayi suka nufi dakinsu tayi musu wanka tasa musu uniform ta fito ta haɗa musu break ɗin sukaci Farooq nata barna shida Muwaddat babu wanda ta isa hanawa yanzun uwarsu tana dawowa su kitsa mata ƙarya da gaskiya ta hau ta zauna ta zage ubanta daya mutu tun batasan kanta ba ta zage uwarta data qare rayuwarta a bauta don rufa mata asiri sannan idan bai isar mata ba ta gama ta da dukan mutuwa wannan yasa take takatsantsan da lamarin gdan. Daƙyar Allah ya taimaketa suka gama ta goya Jannat suka fito ta bawa Isiya lunch box ɗin yaran suka shiga Mota itakuma ta lulluɓe jannat ta koma ta karasa wankin ta shanya ta shiga ta fara gyaran gdan ɗakin Aliyu ne kawai bata shiga ba saboda yayi mata ƙwaƙƙwaran kashedi akan shigar masa ɗaki tun yana gda ko anan ɗinma da Salma taso sakar mata gyaran ɗakin da ita da Salman yacima mutumci dole tasa ta hqr take gyara masa idan ta dawo daga aikinta.

Tana kammalawa da parlourn ta nufi ɗakinta ta gyara ta kwantar da jannat tayi wanka tasa wata jemammiyar atamfarta domin Salma ta hanata Sanya kaya masu kyau kullum kaganta cikin tsumma zaka ishe da hijjab a jikinta batasan dalilin wannan doka ba.
Sai biyu ta shiga kitchen ta manta bata tambayi masu gdan abinda zasu ci ba ta ɗauki wayarta ta kira number Hajiya Salma saida ta katse ta sake kira sannan ta ɗaga cikin masifa tace “wai Anam ke wacce irin wawuya ce ina aiki zaki dameni...." Cikin ladabi tace “kiyi hqr Hajiya mantawa nayi ban tambaye ki abinda za'a girka muku ba....." Da masifa tace dalla Malama bansani ba ni zaki tambaya bazaki tambayi su Farooq ba to ki girka ubanki....." Qit ta kashe wayar Anam ta tsaye sororo da waya a hannunta tanajin ciwon yanda Hajiya Salma batajin nauyin zaginta yanzu daga tambaya sai cin mutumci?
A saluɓe ta nufi kitchen tana tunanin abinda zata girka lumshe manyan idanunta tayi dabara ta faɗo mata tasan Aliyu yanason tuwon shinkafa miyar taushe aikuwa nandanan ta fita tabawa driver sautun kayan taushe wanda babu a gdan ta koma ta ɗora tuwonta ta malmaleshi a leda ta fara tafasa namanta isasshe tasa masa kayan ƙamshi nandanan ta haɗa komanta sannan taja da baya tayi farfesun naman kaji da yaji Attahiru ta jere musu a dinning ta dauko man shanu soyayye ta narka takai musu dinning ɗin.

Shige daki ta zauna tana game da rakani kashinta jin motar masu gdanne yasata miƙewa ta fito

tana riqe da hannun jannat sanye da ƙaton hijjab ɗinta caraf bisa tsautsayi idanunta ya fada cikin na Aliyu tayi saurin janyewa ta rusuna tayi musu Barka da dawowa ya amsa a shaƙe ya buɗe baki yace “hajiya tace kije can gobe Umaimah zatayi birthday  akwai ayyuka acan"
Ajiyar zuciya tayi ko banza ta huta da masifar Salmah ta kwana biyu miƙewa tayi ta koma ɗakinta ta haɗa kayanta a yar ƙaramar akwatu ta dauko ta fito ta canza kaya tasa mayafi har sunyi wanka sun dawo dinning ɗin sunacin abinci ta rusuna tace “na shirya zan tafi" dubanta Salmah tayi tace “kwana uku zakiyi ki dawo" jinjina kai tayi Ta miƙe Aliyu dake satar kallonta yace “ki jirani a waje ganinan"

Jinjina kai tayi ta fita ta tsaya jikin motar ya ɗauki sama da 30 minutes sannan ya fito fuskarsa a murtuke ya buɗe motar ya shiga ya zauna ta buɗe gdan baya zata shiga yace “kinsan dake ni drivern babanki ne shiyasa zaki zauna a baya na tuqaki" bataso ake taɓa mata iyaye yanzun zuciyarta take karyewa ta juya jiki a mace ta shiga motar ya figa a guje ya fice daga gdan suka nufi Danladi na Sidi inda family house dinsu Aliyu yake suna zuwa ta buɗe motar ta fice yabi bayanta da kallo da mugun faduwar gaba ganin yanda take motsa jikinta.
Lumshe idanunsa yayi abin yayi masa dadin gani mamaki ya cikasa yaushe yarinyar ta girma haka har ta haɗa kayan ruwa haka? Saurin jan tsaki yayi yana kawar da tunanin ya fito a motar ya nufi cikin gdan a parlourn Ƙasa ya ishe su ita da Mamanta ta kama mata suna morping yana da hotuna Mama ce taga shigowarsa ta rusuna da girmamawa ta gaisheshi ya amsa kamar yanda yake amsawa da gadara ya haye sama Anam ta taɓe baki tace “kamar wani namijin ƙwarai a gda sai yanda akayi dashi" daƙuwa Mama Yabi ta watsa mata tace malafar ubaki ƴar nema koma mene ai yayi miki rana dalilin zaman gdansa gashinan kema ƴar Sakandire ɗin nan da yara sukeyi kin samu kinyi ta kuɗi to ubaki zakice da Haidar?"

Bata kuma cewa komai ba Umaimah ta fito da wata ƙawarta tana ganinta tace “yawwa Anam ki shiga ɗakina ki gyaramin ki shiryamin wardrobe ɗina kayan sun hargitse" amsawa tayi da to cikin ladabi ta nufi saman tayi sallama Hajiya Muniba tana zaune hakimce a parlourn gaban Anam ya fadi.
Ta rusuna ta gaisheta ta amsa mata a wulaqance tace “Ify" cikin in...Ina tace “Hajiya Umaimah ce tace nazo na gyara mata ɗakinta" jinjina kai tayi ta nuna mata hanya ta miƙe taci uwar ɗammara da mayafin ta nufi ɗakin na Umaimah ta soma gyarawa bayan ta gama ta fito har yanzu suna zaune a parlourn sabanin ɗazu yanzu harda Granny  ta ƙwama uban glass tana ganinta sukayi murmushi a tare tace “ƴar nema jikar na samu kinje kin ɓuya luf abinki Haidar ya boyeki baku Abuja baku Kano zonan naji fatar ki ko tayi laushi"
Dariya tayi da tasa fararen haƙoranta da suka jeru reras da kyakkyawar wushiyar suka bayyana dimple ɗinta ya lotsa tace “Granny tawa bari nazo nayi miki tausar Tailand" Alh Ma'aru dake

gefe yayi murmushi yace “Anam ta Granny nifa Ina tunanin Granny zan dawowa dake su Aliyu sa nemi wata" riƙe baki Granny tayi tace “hooooo Ni Mairamu rufamin asiri da wannan ƴar ƙaniyar ɗiyar tun tana mitsitsiyarta ma azaba take ganamin balle yanzu dubi yanda take wani haɓaka kamar amsawa tsiro taki yo dubi iyayen nonuwa da ɗuwaiwaka idan ta zauneni ai saidai na farka a kabari"

_whattsAp number 09013718241_

*Oum Hairan*
[11/6, 7:22 PM] Oum Hairan&Affan: ME YA JAMIN?

Fauziyya Tasiu Umar
(Oum Hairan)

3-4

Wata baƙar kunya ce ta kama Anam tayi ƙasa da kanta cikin tsananin jin kunya sumsum ta fice Alh Ma'aru yana mata dariya yana cewa “Anam badai kunya ba Hajiya kin bawa yar dakin naki kunya" itadai ƙasa ta sauka taci gaba da taya Mama Yabi aikin da takeyi suna gaf da gamawa Aliyu da Alh Ma'aru suka fito sukayi musu adawo Ify sannan sukaci gaba da ayyukansu basu suka gama ba sai bayan Magrib Anam ta shige ɗakin Mama Yabi tayi alwala tayi sallah ta miƙe a katifa Mama Yabi ce ta shigo masu da abinci ta tashi sukaci suna taba hirar su ta ƴa da uwar suna dariya can Anam ta haɗe rai ta koma kalar tausayi Mama ta dubeta tace tunda kika zo na fahimci damuwa a yanayinki meye ne yake faruwa?" Ƙwalƙwal tayi da ido tace “Allah mama na gaji da masifar Hajiya Salma kullum saita zageki ta zagi ubana da banma sanshi ba ga ƴaƴanta rashin kunya babu kwaɓa kamar ƴaƴan Allah bani musamman Farooq da Muwaddat ji suke kamar zasu iya cin abinci akaina"

Jinjina kai Mama Yabi tayi ta zubawa ƴartata ido tare da sauke numfashi tace “zuwa yanzu ya kamata ace kin saba da waɗannan ƙananun abubuwan Anam ya mutum zaiyi da yanda Ubangiji ya tsara masa rayuwarsa ne saidai ya gode masa kawai in yaki kuma ya godewa

azabarsa don Allah ki koyi haƙuri da yanayin rayuwa komai zai wucce insha Allahu watarana sai kiga labari kike badawa"
Bata da wata sauran kalma data rage da zatayima Mama bayani ta fahimceta dole tasata yin shiru ta kwanta itadai da Dad zai taimaketa kamar yanda ya furta ya dawo da ita gurin Granny tabbas da taji daɗi sosai. Bayan sunyi sallar Isha wani aikin suka dauko ita da Mamanta sukeyin komai cike da kulawa da juna har suka gama wajen 11:30 suka nufi ɗakin Mama suka kwanta sunata yan hirarrakinsu mama tana faɗa mata so takeyi idan Ikcn hutunta yayi zataje Gashua ta kwana biyu rabonta da gida Yobe shekara huɗu kenan kallonta Anam tayi tace “amma meye zai hana mu tafi tare Mama nima inason naje naga dangina"

Dafa kanta mama tayi tace “to banda abinki Kharimatu ai zakije ne kinsan yanayin aikina da naki ba ɗaya bane kedai kije kiyita hqr da halin iyayen gdanki watarana zai zama tarihi kinji" ɗaga kai tayi ta fara addu'ar kwanciya bacci badon taso hukuncin na Mama ba sai don ba halinta bane jayayya da mahaifiyarta da wannan bacci ya ɗauke ta da asuba kuwa suka shiga zarafin aikin abincin birthday duk da cewar an bayar da kwangilar wani amma yanayin yanda suke d yawan masifa gasu da ɗabbaƙa bidi'a yasa gidan ya cika ke kya dauka bikin aure sukeyi ko suna Anam Bata samu kantaba sai huɗu da yammaci tun safe dake Allah ya hore mata Ifyr aiki kamar engine tayi wankanta ta ɗauki wata lashinta da Umaimah ta bata tasa riga ce doguwa saiya kasance sun fito mata da asalin surar ta da ƙuruciyarta abinka da chocolate color oily skin sai milk ɗin less ɗin yayi mugun haskata tayi kyau na ban mamaki ta fita ta nufi sashin Granny ta sameta ita da Alh Mahdi wa gurin Alh Ma'aru ta rusuna ta gaida shi ya amsa mata da sakin fuska Granny tace.

“Ƴar nema kinzo ki tumurmusani ɗin ne?" Dariya tayi tace “haba My Kakus ƴar tsohuwa yaushe rabonki da tausa irin tawa me daɗi saboda daɗinta fah kikece mata tausar Tailand" kama ƙafarta tayi tana matsawa a hankali Alh Mahdi ya tashi yace “Hajiya Iya tunda kin samu ƴar hira bari naje gurin yaran can da suka cika mana gda da kiɗa kamar ƴaƴan yahudawa"
Fita yayi Hajiya Iya da Anam sukaci gaba da hirarsu Hajiya Iya na korarta ita kuma ta nace taƙi tafiya saida tace “zakici kunnen Uwaki bari na kira miki Mala'ikinki Haidar ai yana gdan naga zuwanshi da iyalinshi ƙila na samu salama kajini da ƴa ƴar kusun uwa tanata murɗemin yatsa......"
Wata ƙara Hajiya Iya ta saki daidai Ikcn da Aliyu ya shigo tayi caraf tace “yawwa Haidaruruwa kaɗamin wannan ja'irar yarinyar gurɗemin yatsu take neman yi" kafin ma ya waiwayo kanta tayi wuf ta shige ɗakin Hajiya Iya tana cewa “Granny kefa kikace nayi miki shikenan tunda bakiso bari na gyara miki ɗakinki na jera miki kayanki a wardrobe"

Bata kula da hararar da Aliyun ke watsa mata ba shi yarasa meye tashi batazo ɗaya da yarinyar

ba yanda ta nufi ɗakin tana kaɗa jiki yayi mugun ƙular dashi a haukansa gani yake donshi takeyi wanda ita batasan ma da hakan ba tunda bata taɓa samun mai faɗi mata ba. Tana jiyo hirarsu da Granny yau ma kamar kullum Ƙorafi takeyi masa shi yaƙi gaba kullum kaganshi kamar haɗowar hadari bayada fara'a baya da rahama a fuskarsa inda shi kuma yace “nikam Granny kinsamin ido da yawa duk duniya kece kike cemin na ragu kona ƙaru ke kuma ba iya yimin maganin matsala ta zakiyi ba"........
Sunata hirarsu da zolayar juna yanata dariya abinda kullum yake bawa Anam mamaki ko a gdansa ita zata iya rantsewa bata taɓa ganinsa yana dariya ba kullum fuskarsa kamar ta bijimin sa amma Indai ya haɗu da Granny yanzu zakijishi yana ɓabɓaka dariya, taɓe baki tayi a ranta tace “miskilin banza da baya iya control na gdansa a fili kuma amsa kiran da Granny take mata tayi ta fito tana goge fuskarta da tsumma ta rusuna tace “gani Kaka" nuna mata kitchen tayi tace “wannan kitifaffen ubangidan naki zaki haɗowa abinci yace anan zaici"
Miƙewa tayi ta nufi kitchen ɗin yana latsa wayar hannunsa ta haɗo sinasir da miyarsa da taji tantaƙwashi da man shanu ta dauko masa lemu me sanyi da ruwa ta jero masa ta nufo inda yake gabanta na faɗuwa ko a gda bata ƙaunar kai masa abinci saboda baayi masa gwaninta. Tsugunnawa tayi a gabansa mayafin jikinta ya zame daga kanta dake me yauƙi ne ya sauka ƙasa bisa rashin saa rigar irin me buɗaɗɗen wuyan nan ce tudun dukiyar fulaninta duk a waje suke hakan yayi daidai da ɗagowarsa da nufin yi mata masifar daya saba tsautsayi yasa idonsa ya caki ƙirjinta da batama lura da mayafin ya zame ba ya zubawa wannan abu me matuƙar ɗaukar hankalinsa a jikin mace idanu kamar wanda ya warke daga ciwon makanta, hakan yayi daidai da ɗagowarta da nufin neman izinin tashi domin ta gama haɗa masa kawai ta mayar da idanunta a ƙirjinta taga abinda ya shagala da kallo. Ta kuwa firgita ainun a razane ta wawuro mayafinta ta rufe jikinta ko ina na jikinta ya ɗauki rawa tasan yau ta shiga uku har shida gaban shida har tara ma ta shiga.

[11/6, 7:22 PM] Oum Hairan&Affan: ME YA JAMIN?

Fauziyya Tasiu Umar
(Oum Hairan)

5-6

Cikin kiɗima ta ja da baya ta zube a ƙasa tayi knile down  tace “kayima girman Allah da darajar Hajiya da Alh kayi hqr wlh tallahi bansan ya zame b......" Ɗaganta hannu yayi ya haɗiye kunyarsa cikin ƙara ji yace “tashi kibani guri mara sanin ciwon kai wato ke nan har kinkai budurwar da zaki rinƙa tallan jikinki a kwararo toni ko jiki zai burgeni me zanyi da wannan baƙar fatar taki wawuya dake bagidajiya"
Itadai Anam har tuntuɓe takeyi saboda sauri sukayi kicibis da Granny ta riƙota da sauri tana cewa “ke marainiyar Allah nutsu kama kanki meye yayi zafi da wannan firgici haka me Haidar

ɗin yayi miki?" Toshe bakinta tayi domin batada kalmar magana ta janye ta kwasa a mugun guje ta nufi bayan gdan saida ta fakaici ido sannan ta shiga gdan ta shige ɗakin Mama Yabi cikin Sa'a itanma batanan ta kwanta tana mayar da numfashi tare da yima Allah gdy daya kuɓutar da ita daga cin duka gurinsa tananan kwance har aka gama birthday ɗin kowa ya watse saida ta tabbatar da tafiyar Aliyu da Salma sannan ta fito suka shiga gyaran gdan basu gama ba saida dare ya shiga suka ƙarasa suka kwanta .

Washegari ma aikin ne dasu Hajiya Muniba irin matan nan ne da baayi musu gwaninta komai kayi baka iyaba su gyara nan tace ba hakaba su gyara nan tace a'a daƙyar Allah ya basu ikon gamawa itama wannan rana sunji a jikinsu dan ko abinci basu samu damar ci ba sai Magrib suna cikin cin abincin Umaimah ta shigo ta dubeta tace “Ya Aliyu yace kije ku tafi gobe Monday sunada aiki" wani abu ya tokare mata maƙoshi abincin data zuba a bakinta yaƙi haɗiyuwa a ranta tace “shikenan shi bawa bashi da hutu bashi da ƴanci a rayuwarsa?
Mama ce ta taɓa ta tace “ki tashi karkiyi laifi Haidar ba wuya bane fusatashi" miƙewa tayi sarai tasan halinsa ko kayanta bata ɗauka ba ta fita yana zaune cikin mota ta nufi motar gabanta na faɗuwa da kuma matsananciyar kunyarsa ta isa ta buɗe ta shiga bata ko samu arziƙin kallo ba ya gama wayarsa yatada motar suka tafi har sukaje gdan bai tanka mata ba yana parking ta fita yabi bayanta da kallo tare da taɓe baki.
Turus taja ta tsaya saboda ganin yanda parlourn yayi kaca² yaran duk sun ɓatashi da gudu Jannat ta nufota ta ɗauke ta tana juyawa da ita tanayi mata dariya yarinyar ma na dariya daidai Ikcn da Salma ta fito Anam bataji tahowarta ba kawai sukayi karo aikuwa ta angajeta bisa tsautsayi ta faɗa kan cup ɗin glass ɗin ɗaya fashe a parlourn aikuwa ta fasa ƙara saboda nitsewar da kwalbar tayi a goshinta jini yayi wata irin tsartuwa ya fallatsa har jikin Aliyu dake tsaye tun Ikcn da Anam keyima Jannat wasa.

Da gudu ya ƙara so kanta ya ɗagota gabaɗaya jini ya wanke mata fuska yace “subhanallahi Salma bakida hankali ne wasa fa takewa ƴarki shine zaki ture ta har kiji mata ciwo haka kefa kika dameni naje na ɗaukota yara sun dameki dama abinda kika shirya yi mata kenan?"
Yana mgn yana tare jinin da hannunsa inda ita kuma Anam taketa jijjiga kanta daya ɗaure da wani mugun ciwo, taɓe baki Salma tayi tace “to ko zaka rama matane Aliyu naga alamun kaji ciwon kaima a jikinka" kallon Salman yayi rashin Ikcn bata amsa yasashi kama hannun Anam yace “Sannu Kharimatu tashi muje ayi miki dressing na gurin" miƙewa tayi tana layi saboda ba ƙaramin jini ta zubar ba motar yaja a mugun guje suka fice daga gdan suka nufi wani asibitin kuɗi a cikin unguwar ta Yankaba tasha wahala kafin su zare kwalbar sukayi dressing gurin likitan ya dubesa yace “zatayita fama da ciwon kai dole ta rinƙa samun hutu" jinjina kai yayi ya biya su suka fito har yanzu kuka takeyi bawai na zafin ciwon bane a'a tunawa da tayi cewa da mahaifinta yana raye qila duk da haka bata rinƙa faruwa da itaba.

Sau ɗaya yace mata sannu har sukaje gda wani abin mamaki Salma Bata gyara gurin da jinin ya zuba ba balle ta gyara parlourn Suna shiga Anam ta ɗauki tsintsiya zata share parlourn ya dakatar da ita yace “kije ki kwanta kawai" aje tsintsiyar tayi ta nufi ɗakinta ta kwanta nandanan kuwa zazzaɓi ya rufeta me zafin gaske a daren taci wahalar zazzaɓin batayi tunanin zatakai safe ba hakanan dai ta rinƙa addu'o'in da suka sawwaƙa a bakinta har zuwa wayewar gari da safe da wuri ta tashi domin shirya yaran zuwa makaranta ta kamasu tayi musu wanka tanayi tana duba breakfast ɗin data ɗora harta gama ta haɗa masu gdan basu sauko ba ta zauna tana rawar sanyi tana bama yaran abinci zazzaɓi na ƙara ƙarfi sanyin A.C na haɗa ta ita ba abin ta kasheba matar gdan ta nakasata.
Gama sallamar yaran tayi takaisu ga driver ya tafi makaranta dasu hadda jannat dake itama ansata juma'a ne bata zuwa ta dawo a wahalce ta rinƙa gyara gdan ta kusa gama parlourn taji sun sauko ta durƙusa cikin ladabi ta gaishesu  Salma ta ɗauke kai sai Aliyu ne yace “ya jikin...." Kafin ta bashi amsa yaga yanda take rawar sanyi yace “ko zazzaɓi kikeyi ne?" Ɗaga masa kai tayi ya matsa ya taɓa jikinta yaji zafi zau ya dubi Salma yace “ki ɗauki key na motarki ki tafi zan Kaita asibiti" wani malolon baƙin ciki ne ya cika zuciyar Salma ta kuwa taso masa da cewa “haba Aliyu wannan ai wulaƙanci ne akan wannan ƙazamar talakan  zakace naje nayi driving bayan kasan banason......."

Ɗaga mata hannu yayi ya dubi Anam yace “Ɗauko hijjab ɗinki Kharimatu" da sauri ta miƙe domin shiga ta ɗauko hijjab ɗin jiri ya ɗebeta ji kakeyi tik ta zube a ƙasa ya isa da gudu ya ɗagota ya fice da ita yasata a mota suka fita suna zuwa aka bata gado tsoron kira yake ya faɗa yasan masifar Granny Indai tasan dalili to ba Salma ba shi kansa ya kaɗe har ganyensa.
Ganin Ikc na tafiya gashi yanada taro 9:30am yasashi yin shahadar kiran wayar Mama Yabi ta ɗaga suka gaisa ya faɗa mata abinda ke faruwa aikam ta ruɗe tace “bansan yaushe Kharimatu zatayi hankali ba kawai saboda sakarci taje zata illata kanta ganinan"
Ajiyar zuciya yayi ganin ya ɗorata ta ɗoru yaci gaba da zama gurin Anam tare da zubanta ido yanda take kwance da drip a hannunta baccin wahala ya ɗauketa kanta sanye da hula fuskarta wasai ga ɗaurin dressing ɗin da akayi mata jiya a hankali ya gangaro zuwa gangar jikinta yana ƙare mata kallo tunda yake baitaɓa tsayawa ya ƙarewa Anam kallo ba sai Yau Nazeer abokinsa yana yawan faɗa masa wato Aliyu babyn nan ta gdanka Anam tana matuƙar burgeni ɓoyayyen kyaunta yana ruɗani bantaɓa gajiya da kallonta ba nikam da zan samu dama zanso abani wannan yarinya matsayin mata nasan zanji daɗin hakan" taɓe baki yayi ya miƙe yana ƙare mata kallo yace “kai kasan wani ɓoyayyen kyau Nazeer Ni bayyananne na sani".......

_Zaku iya samun damar cigaba da karanta wannan littafi kan ₦300 kacal tura ta acc 0255526235 Gtbank ko kati MTN ta whattsAp number 09013718241_

*Oum Hairan*
[11/6, 7:22 PM] Oum Hairan&Affan: ME YA JAMIN?

~Paid book~

Oum Hairan

7-8

Kiciɓis sukayi da Mama a ƙofar shiga ɗakin suka gaisa ta shige ciki ta zubawa ƴartata ido cike da tausayi ƙarasawa tayi gabanta ta riƙo hannunta daidai lkcn data buɗe idonta tace mata “sannu Kharimatu ashe haka tsautsayi ya faru dake kema kin cika gaugawa ki rinƙa bin abubuwa a hankali kinji" lumshe idonta tayi tanajin ɗacin abinda ya faru da ita a ranta Aliyu ya shigo da sallamarsa a ƙasan maqoshi ya ajiye ruwa da magunguna yace da Mama “tunda kinzo zanje office inada Meeting zuwa tara da rabi" kuɗi ya zaro ya ajiye a gefen gadon tayi masa gdy ya fice a ɗakin batare dako inda Anam take ya kalla ba.
Bayan fitarsa Mama ta haɗa mata shayi me kauri da madarar daya kawo ta zauna tana bata tanaci daƙyar abincin ɗaci yakeyi mata a baki hakadai ta rinƙa turawa harta ƙoshi jefi² suke yar hirarsu da Mama Anam ta kasa jurewa ta faɗawa Mama asalin abinda yaji mata ciwo har ya haifar mata da zazzaɓin sosai Mama taji babu daɗi amma a fili sai tace “babu komai akwai Allah da talaka da mai arziƙi duka wanda yayi su son abinsa yakeyi saboda haka komai yayi farko zaiyi ƙarshe"

Ba haka Anam tasoba domin zuwa lkcn hƙrnta da zama a gdan Salma ya ƙare burinta kawai barin gdan saidai batada wata hanya ta barin gdan dole saida shahalewar Mama, yini sukayi a asibitin da yamma Aliyu ya dawo shida Granny tanata zubawa Anam sannu likitan yazo ya sallameta yayi Hamdala domin bayaso asirinsu ya tonu yafiso ayi a lulluɓe mgnr ɗebe kayan sukayi suka zuba a mota bayan sun shiga Granny tace “Ali wannan yarinyar gda zata wucce gurin uwarta idan ta warke ta dawo wannan kasaltacciyar matar taka me shegen son jiki ba ƙyaleta zatayi ta warke ba"
Bayason jan maganar dole ya amince saboda gudun tujarar Granny suka wucce Ɗan ladi nab

Sidi zuciyar Mama da Anam wasai suna zuwa ya zubesu ya juya ya nufi gdansa. A falon ya tarar da Salma taci uwar kwalliya ta harɗe tana kallo tanacin donnut ya dubi yaran yagansu da kayan islamiyya yace “ya haka Salma gobe babu makaranta ne?" Ɗagowa tayi tace “kayan naji suna tsamin gumi shine nabarsu idan kun dawo waccen yarinyar ta wanke" jinjina kai yayi lallai Salma batada imani wato wadda aka sallamo a asibiti take tsammanin tayi mata wanki lallai Granny tanada hangen nesa.

Samansa ya haye yayi wanka ya fito ya zauna a dinning ya buɗe abinci ya faraci baici na kirki ba ya miƙe ya nufi waje ya zauna a kujerun dake cikin flowers na gdan yana duba jarida
Bai koma cikin gdan ba sai bayan yayi sallah Magrib da isha sannan ya shiga ya nufi saman ya shiga ɗakinsa ya sake watsa ruwa ya kwanta shiru yana jiran Salma har dare ya tsala yaja tsaki ya juya lamarin Salma ta fannin kula da shimfiɗarsa yana bashi tsoro kullum ita cikin uzuri take yau aiki gobe ciwon mara jibi zubar jini idan bataga damaba sai su shafe satittika a haka babu ruwanta shikuma ga miskilanci Indai bata kawo kanta ba ya daina kiranta.
Wayewar garin ta shirya tsaf tana mita ta shirya yaran suka fice suka tafi aiki sukuma yaran aka wucce dasu makaranta a mota take tambayarsa wai meye ya hana Anam dawowa? A gajarce yace “ganin dama" daga haka tayi masa shiru shima yayi mata ya ajeta a ma'aikatarsu ya wucce Campanynsu.

Kwanakin da Anam tayi tare da Mahaifiyarta abin gwanin daɗi ji takeyi kamar karta koma. Ranar data cika sati tana ɗakin Granny sunata shirmensu Suka tsinkayo sallamar Aliyu saida gabanta ya faɗi ya shigo ɗakin idanunsa na kanta hakanan ya riski kansa da wata muguwar faɗuwar gaba Ikcn da ya sauke idanunsa akanta cikin sati gudan da baya ganinta sai yaga gabaɗaya ta canza masa tayi wani haske fuskarta tayi fiyau da ita, janye gashinta tayi daga hannun Granny da take daure matashi tana ranƙwashinta tana cewa “ni banda tsiya Allah yayi miki yalwar suma ki rinƙa neman lalatata da shirme idan tayi fushi ta kaɗe ai naga da uwar da zakiyawa mijin da kishiyar gwalli"
Turo baki tayi tace “tabdi lallai ma Granny nikam ki dainamin fatan kishiya wlh ko sunan banson ji" ba Granny ba hatta Aliyu saida ya zare tabarau ɗin idanunsa ya kalleta tayi ƙasa da kai ganin irin kallon da yakeyi mata yasata jan mayafinta ta fice sumsum har taje bakin ƙofa yace “ki shirya zamu tafi gdan babu kowa Salma ta tafi Ziyarar aiki Sokoto sai yara"

Amsawa tayi cikin ladabi duk da bataso hakan ba amma ya zatayi ta fice ta nufi cikin ta ishe Hajiya Muniba a parlour tayi mata sannu da gda ta amsa mata a yatsine ta wucce ta tarar

Mama hatta haɗe mata kayanta dauka kawai tayi tana hawaye ta fita daidai Ikcn da yake fitowa a sashin Granny ya shiga gdan bai jima ba ya fito ya shiga motar itama ta shiga suka wucce. Yaran sai murna sukeyi ta dawo itakuma tana ƙunci sarai Aliyu ya lura bataso dawowar ba daga yanayinta baisan dalili ba duk sai yaji ya tsargi kansa da takura mata to amma ya zaiyi zaman gda daga shi sai yara bazai yiwu ba itakuma Salma yanayin aikinta yana yawan sasu yawo. Kayanta ta ɗauka ta shige ciki yabita da kallo shi kansa baisan meye yake kallo a jikinta ba amma tabbas yasani ba tun yau ba wani abu yana burgeshi game da yarinyar a hankali batare daya sani ba ya kira sunanta taja ta tsaya cikin fargaba tare da juyowa shikansa baisan dalilin kiran ba yace "am ki dafamin coffee ki kawomin ɗakina" saida taji wani ras da yace ɗakinsa domin a tarihin zamanta na gdan batajin ta taɓa shiga ɗakinsa yananan bai bata dama ba har marinta saida yayi akan aikenta ma da Salma takeyi tun Ikcn ta daina gigin zuwar masa ɗaki........

_Zaku iya samun damar cigaba da karanta wannan littafi kan ₦300 kacal tura ta acc 0255526235 Gtbank ko kati MTN ta whattsAp number 09013718241_

*Oum Hairan*
[11/6, 7:22 PM] Oum Hairan&Affan: ME YA JAMIN?

Paid book

Oum Hairan

9-10

Shiga tayi ta aje kayan ta fito ta nufi kitchen yaran suka biyo ta musamman Farooq yana ce mata "nifa yunwa nake ji daddy indomie kawai ya bamu" jinjina kai tayi ta kunnan kan Gas biyu ɗaya ta doransa coffee ɗaya ta ɗora abinci ta riga gama dafa masa coffee ɗin ta ɗauka ta nufi ɗakin nasa ta ƙwanƙwasa yana zaune ya zuba uban tagumi baisan abinda zuciyarsa take shirin aikatawa ba amma tabbas tana tunzurashi ya aikata wani abu saidai shi kansa yanajin faɗuwar gaba idan ya tuna abin mai wahalar yuwuwa ne bayan haka ma zuciyarsa kamar ba adala bace a cikin sati guda tunanin nan ya fara bijiro masa wanda ya ɗarsu domin nemawa yaransa mafita shin tayaya ma Anam zata amince da wannan shirin nasa? In itan ta amince mahaifiyarta da

mahaifansa zasu yarda? Musamman ma Hajiya Muniba.

Ya jinjina wannan lamari yafi a ƙirga kafin ya ankare da taɓa ƙofar da akeyi yabata izinin shigowa ta buɗe ta shigo da sallama a bakinta amma kanta a ƙasa yake ta ajiye masa flat ɗin data jero kofunan ta miƙe zata fita yace “am bakiji ba...." Tsayawa tayi tare da juyowa ta koma ta tsugunna tace “Na'am" zubanta ido yayi ya kuma kasa cewa da ita komi har saida ta gaji tace “Abinci na ɗorawa su Farooq zai iya ƙonewa"
Numfashi ya sauke ya bata izinin tashi ta miƙe ta fita ta koma kitchen ɗin ta tace shinkafar data ɗora ta zuba musu miyar data dumama ta ɗauka suka fito Parlourn tana bawa jannat Muwaddat da Farooq sunaci yanda yaran sukecin abincin zai tabbatar maka da gaske yunwa sukeji.
Sunci abincin sosai ta gyara gurin ta jasu ɗakinsu ta kwantar dasu bayan tayi musu wanka itama tayi tayi sallar Magrib da isha da bata samu tayi ba ta kwanta a cikinsu tana rungume da Jannat tayi musu Addu'a bacci ya ɗaukesu dukkansu.

Fitowa yayi domin duba yaran ya buɗe ɗakin ya shiga tare da kai hannu ya kunna glub gabansa ya fadi ganinta kwance tsakiyar yaran ya daɗe tsaye yana kallonta luguden zuciyarsa na ƙaruwa a kallo na zahiri baya hango wani abu dake burgeshi ga Anam Amma ya fahimci zuciyarsa ta jima da sanya masa wasu alamomi masu neman fassara.
Juyawa yayi ya fice zucciyar tasa cike da tunanin ta inda zai fara aikinsa tabbas lkc yayi da ya kamata ya samawa yarinyar yanci wanda ya farajin ɗarsuwar dacewar sa daga tausayi, ya ɓata dogon lkc yana tunanin rikicin da yake shirin ɓallowa kansa da Anam Amma zuciyarsa taƙi karaya a ƙarshe wayarsa ya ɗauka ya turawa abokinsa Nazeer cewar gobe su haɗu a office yanason su tattauna. Hakance ta faru washegarin kamar yanda Anam ta tashi da wuri haka shima ya tashi lkcn daya fito tana kitchen tana haɗa abin karin safe tana goye da Jannat da tayima wanka ta juyo ta ganshi tsaye a ƙofar kitchen ɗin ta sunkuyar da kanta tare da gaisheshi cikin ladabi ya amsata yace “ina sauri ne" daga kai tayi tare da ɗaukar kayan data gama dasu takai dinning ta dawo ta gyara kitchen ɗin ta shirya yaran ta miƙawa driver su ya tafi kaisu makaranta hakan yabata damar sake kwanciya.

*********

Duban juna sukeyi da Nazeer kowa yana sauke numfashi inda Nazeer yake goge zuffa ya ɗago cikin tsananin mamakin abokin nasa yace “ƴar aikin gdanka kakeji kanaso kuma so na aure? To ya kuma zakayi da masifaffiyar matarka me ɓaƙin kishin masifa?"
Ajiyar zuciya ya sauke ya aje biron da yake wasa dashi a hannunsa yace “abinda nakasa

samun amsarsa kenan am ni Ina ganin idan harsu Hajiya sun amince bazai zama matsala ba asanya rana gajeriys cikin sirri zanyi ƙoƙarin nema mata gida ƙarami nasata a ciki kafin komai ya daidaita bansan meye yake damun mata ba sun gaza ta ɓangarori da dama na auratayya amma daga lkcn da namiji yayi niyyar ɗauko musu wacce zata tayasu sai suyi tsalle suce basusan zancen ba duba dai Nazeer kaga rayuwar gdana nasani duk da cewar Salma Bata cikin matan da zaayima tambarin ƙazanta Amma fah da taimakon Anam kullum kaje gdannan Anam Bata tsaye bata zaune itace kula da yara gda da masu gda to inda zata iya ɗaukar wannan aikin meye yasa bazan gayyato ta tazo ta tayamu rayuwar har abada ba? Am Bama wannan ba Nazeer duk da cewar Ni bana cikin jinsi na maza masu takura ko yawan buqata hasali ma ta wannan fannin inada rauni amma fah a hakan duk lkcn dana buƙaci Salma sai ta kawomin uzuri kuma fah duk da haka cewa takeyi Ni ragone"

Shafa ƙeya Nazeer yayi yace “hakane
saidai kasan tunanin mata ya bambanta da namu sukan a ɓangarensu wannan babban abin kunya ne zaka aikata tabbas za'ayi surutu Bama iyakar surutu ba harda abinda yafi surutu to amma dake ka shirya saika fita da qwanjinka idan rabone sai kaga ka dauka"
Miƙewa sukayi tare suka fita sun jima jikin mota suna ƙara tattaunawa sannan sukayi musabaha suka rabu kowa ya shiga motarsa lkcn da yaje gda bai iske kowa ba a parlour ɗakinsa ya shiga ya cire kayansa ya watsa ruwa ya sanya jallabiya ya sauko ƙasan ɗakin Anam ya nufa ya ƙwanƙwasa ta  miƙe a gyaran wardrobe ɗin da takeyi ta buɗe yana tsaye da cup a hannunsa ya zubanta idanunsa masu kama da wanda kejin bacci ta sunkuya cikin nutsuwa tace “barka da dawowa" lumshe idonsa yayi yanajin muryarta na ratsa sassan jikinsa yace “ina yaran nan?"
Sunkuyar dakai tayi tace “dake juma'a ce Zeeze tazo ta ɗaukesu wai Aunty Salma tace tazo ta ɗaukesu suyi weekend acan"

Jinjina kai yayi yace “ina buƙatar abinci" yana faɗin haka yayi gaba ta koma ciki ta ɗauka hijjab ɗinta ta fito ta shiga kitchen ta haɗo masa abincin ta kawo masa ta miƙe zata tafi yace “bakiji ba" tsayawa tayi yace “ki haɗa kizo ki zauna inason mgn dake ne" dawowa tayi ta zauna ta fara haɗa masa a zahiri zakace wayar hannunsa yake kallo amma Anam ya zubawa idanu yana nazarinta sanyin yanayinta yafi komai burgeshi a ƴan kwanakin nan mika masa flat ɗin tayi cikin natsuwa yasa hannu ya karba tare da saukowa ƙasa ya zauna ya tanƙwashe ƙafarsa yanacin abincin yana satar kallonta, duk ta tsargu so take ya sallameta ta tafi gashi taga alamun bashi da niyyar bata izinin tafiya.
“Ranar da naje ɗaukoki a gda naji kinyi mgn lkcn da Granny take Miki faɗan gyara gashi kince ta daina yi miki fatan kishiya ko zan iya sanin dalilinki?"
Kanta na ƙasa ta ɗago ta sake sunkuyar dakai bazata iya jurewa irin kallon da yakeyi mata ba hakan yasa duk ta takura
Alamu yaga na bazatayi mgn ba yasashi cewa “ok amma zaki iya auren me mata?" Ɗagowa

tayi da mugun sauri tare da girgiza masa kai ba tare da ta san tana girgiza masan ba kafeta yayi da idanunsa cike da faduwar gaba yace “why?" Maimakon ta bashi amsa sai kawai yaga ta fara share hawaye ya sake zubanta ido yace “talk me mana" ƙasa tayi da idanunta tace “ni kawai banaso ne saboda bazan iya fitina da tashin hankali ba kuma...kuma...." Shiru tayi
Tana qorarin haɗiye mgnr yace “kuma me?" Sake jan zuciya tayi tace “idan bakada galihu Gara ka samu mijinka kai ɗaya kada kaje ka shiga inda za'a ke maka gori" da sauri ya dubeta yace “gorin me?" Shiru tayi masa alamun tagaji da tambayar yayi murmushi ya matso gabanta yakai hannunsa kamar zai kamo nata tayi saurin janyewa cike da tsoro kawar da hannunsa yayi yace “yanzu idan ya kasance wani mutum me daraja da yasan ƙimarki yasan mutuncinki ya fito yace yanason aurenki sai ya kasance yanada mata da yara amma yace bazai hadaku gda ɗaya ba zai ware miki mazauninki daban shin zaki iya amincewa da hakan ko har yanzu baki gamsu ba?"

Shiru tayi gabanta na faɗuwa yayi murmushi yace “life hakanne zai faru wato akwai wani da yayimin mgn akanki kuma na yaba da nutsuwarsa so sai naga dacewar neman jin ra'ayinki game da hakan kafin a shigar da mgnr ga Mama so me kike gani akai yacemin bai buƙatar jan lkc a shirye yake kuma da gaske yakeyi"
Tunda ya kawo mgnr wanin gabanta ke faɗuwa wani tsoro yana shigar ta ta ɗago tana girgiza masa kai tace “Yallaɓai nikam banason auren me mata inajin tsoron kishiya amma idan ka yaba da nutsuwarsa banida ja zan roƙi Allah ya sanyamin dangana ya ciremin tsoron a zuciyata" murmushi yayi yace “good haka nakeso kije ki kwanta saida safe" kamar me jiran ya bata umarni ta miƙe ta nufi ɗakinta yabita da kallo yana murmushi yarinyar akwai nutsuwa shi mamakin ta inda ta samu wannan tarbiyyar yakeyi duk da kasancewar uwarta batada sauƙi wajen tarbiyya amma yawanci irin yaran nan da suka taso a wahalce zaka samesu basu cika nutsuwa ba tabbas idan yayi nasarar mallakar ta zai samu cikakkiyar kwanciyar hankali........

_Zaku iya samun damar cigaba da karanta wannan littafi kan ₦300 kacal tura ta acc 0255526235 Gtbank ko kati MTN ta WhatsApp number 09013718241_

*Oum Hairan*
[11/6, 7:22 PM] Oum Hairan&Affan: ME YA JAMIN?

~Paid book~

Oum Hairan

Free 11-12

_promo ya sauka💃_ _Littafaina biyu da nakeyi yanzu haka YAFI ZAMAN AURE da ME YA JAMIN? A baya regular na kowanne 300 ne VIP 600 so yanzu abun ya canza idan ki/ka nason duka biyun regular zakiyi subscribe da ₦400 ne VIP kuma duka biyun zaki biya ₦700 ne wannan ya faru ne sakamakon wani dalili wanda garabasar zata ƙare daga ashirin ga watannan ne so ku hanzarta biyan naku maimakon ₦900 vip 2 books ya koma ₦700 regular 2 books ya koma ₦400 tabbas sai me rabo._

_Zaku iya samun damar cigaba da karanta wannan littafai ta hanyar biyan kuɗinku ta 0255526235 Gtbank ko kati MTN ta WhatsApp number 09013718241_

________________________________

Tunda ta shiga ɗakin take kaiwa da komowa ƙirjinta sai bugawa yakeyi Allah ya jarabceta da mugun tsoron kishiya itakam batason kishiya badon komai ba sai don gudun fitina musamman yanda zamani ya zama kawai suna marnege na rayuwarsu ita da mahaifiyarta aje a illata akan namiji......
Zama tayi a gefen gadon ta ɗaga hannunta sama tace “ya Allah ka zama gatana a duk inda ka sanya rayuwata tabbas kaine sarki mafi iya hukunci ga bayinsa kaine mafi cikakken zaɓi da iko" tana faɗin haka ta kwanta ta lumshe idanunta maganganun da sukayi da Aliyu suna dawo mata bata bawa sanin mutumin da yake bata lbr muhimmanci ba saboda haka ta gyara kwanciya taja bargo ta ƙudundune baccinta me daɗi na kwanciyar hankali ya ɗauke ta gobe zata huta babu yara babu matar gdan sai megidan shikam ba fitowa yakeyi ba weekend sai 12:00pm hakan yasa taji a ranta zata sarara na 2 days.

Washegari sai takwas tayi wanka ta fito ta gyara parlourn ta nufi kitchen ta ɗora break sai bayan ta gama ta fahimci ashe Aliyun baya gdan ta jere a dinning ta nufi ɗakinta ta zauna taci nata hankali kwance bayan ta gama tayi wanke² ta sake gyara inda ta ɓata ta kuma kwanciya bacci ya ɗauketa sai azahar ta farka tayi sallah ta wucce kitchen shiru babu Aliyu babu labarinsa haka ta ɗauki abincin safen ta kaiwa masu gadi sannan tayi wani.
Ta gama girkin kenan taji tsayawar motarsa ta ɗauki hijjab ɗinta ta zura ya shigo ta fito a kitchen ɗin ta durƙusa tace “barka da shigowa yallaɓai" wata gwauruwar ajiyar zuciya ta dubeshi da sauri yayi mata murmushi batare da yace komai ba ya nufi saman saida yaje step na ƙarshe sannan yace “ki kawomin coffee da abinci nasha wahala yau garinku sunada tsaurin Al'ada" “garinmu kuma?" Ta faɗa a zucci tare da juyawa ta shiga kitchen ta haɗo masa duk

abinda tasan zashi buƙata ta nufi saman tayi knowking yabata izinin shiga yana zaune a parlourn nasa daga shi sai boxes ko arziƙin riga bashida sai suma da tayima ƙirjinsa riga tayi saurin ɗauke idonta cike da faduwar gaba ta aje kayan jikinta na rawa ta juya zata fita yace "Kharimatuh" tsayawa tayi ba tare data juyoba yana numfashi yace.

"Dole takunki ya canza ki kula da kanki sosai kuma kiyi hƙr da duk abinda ka iya faɗowa rayuwarki a wannan lokacin ki sani keɗin ba Kharimatun da bace yanzun akwai wani gingimemen nauyi akanki wanda idan kikayi wasarairai dashi tabbas Ubangiji ka iya azabtar dake da haƙƙinsa ba kowanne irin nauyi aka ɗora miki ba face igiyar aure......."
A mugun firgice kuma a kiɗime ta juyo jikinta da bakinta na ɓari tace "au....aure...." Murmushi yayi mata yace "Yeah aure Kharimatu tabbas yau cikin iko na Ubangiji kin tabbata matar Barrister Aliyu Ma'aruf Gusau......" Batasan sanda ƙafafunta suka zubar da ita a tsakiyar ɗakin ba cikin sarƙewar Harshe take furta "Innanillahi wa Inna ilaihirraji'un" kasa sake furta kowacce kalma tayi saboda tsabar birgici da tashin hankali inda shikuma yaja butar coffee ɗinsa ya tsiyaya yakai bakinsa ya lumshe idanunsa ya sake kurɓa sannan ya sauke yace "tabbas kamar yanda abin ya daki zuciyarki ya daki zuciyar kowa ma daya sani musamman Hajiyata da Mama da ƙanne na bansan lkcn da hakan ta faru ba bansan meye ya janyo ba nidai a daren jiya naje na sanar da Granny yanda mukayi dake domin nasan itace kaɗai zata goyamin baya sannan zatasa kowa taga dama yayi ko baiyi niyya ba bayan na taho a daren ta shigar da mgnr ga Dad so shima baija ba yaji daɗi sosai yace idan an sanar da Mama sai aje a nemamin aurenkin.

Aikam a lkcn Granny ta kira mama da Hajiyata ta sanar dasu dukkansu sunso suyi tsalle wai bazai yuwu Salmah ta raineki kuma ki aure mata miji ba zaman bazai taɓa daɗi ba saida Granny ta hau kan Hajiya sannan ta hƙr tace itafa ba ƙinki takeyi ba kawai dai tana jiye miki abinda kaje yazo ne, Itako Mama Yabi ƙin amincewa tayi saida taga ran Granny ya ɓaci sannan ta aminta so da safennan Dad ya kirani yace nazo nakai Mama Guru sanda naje hatta tafi sai yace muje nida Baba Labaran da Nazeer dashi haka muka tafi bansan meye za'ayi ba saida mukaje suke faɗamin an sanar da kakanki ne a daren jiya yace azo da sadaki da kuɗin turare al'ada dai taku ta barebari zai ɗaura aure gobe.
Wannsn ne ya kawo aka ɗaura aure na dake a yau Kharimatu....."
Kuka ta rushe dashi me gunji cikin kukan take cewa "nikam banyi marhabun da wannan auren ba wannan wanne irin rashin yanci ne wlh ban yarda ba ban amince ba banason auren nan don Allah Daddy Farooq ka rufamin asiri kada Aunty Salma taji ta kasheni wlh taci alwashin duk matar data auri mijinta saita kasheta a gabana tasha furta wannan kalmar meye yasa Ni zan jefa kaina......

*Oum Hairan*
[11/6, 7:22 PM] Oum Hairan&Affan: ME YA JAMIN?

~Paid book~

Oum Hairan

Free 13-14

_promo ya sauka saura kwana biyu rak👌🏻💃_ _Littafaina biyu da nakeyi yanzu haka YAFI ZAMAN AURE da ME YA JAMIN? A baya regular na kowanne 300 ne VIP 600 so yanzu abun ya canza idan ki/ka nason duka biyun regular zakiyi subscribe da ₦400 ne VIP kuma duka biyun zaki biya ₦700 ne wannan ya faru ne sakamakon wani dalili wanda garabasar zata ƙare daga ashirin ga watannan ne so ku hanzarta biyan naku maimakon ₦900 vip 2 books ya koma ₦700 regular 2 books ya koma ₦400 tabbas sai me rabo, saura kwana biyu rak👌🏻💃._

_Zaku iya samun damar cigaba da karanta wannan littafai ta hanyar biyan kuɗinku ta 0255526235 Gtbank ko kati MTN ta WhatsApp number 09013718241_
_Yan Niger kuyi mgn ta wannan number domin biyan naku 94775574_

---

*Oum Hairan*
[11/6, 7:22 PM] Oum Hairan&Affan: ME YA JAMIN?

~Paid book~

Oum Hairan

Free 15-16

_promo ya sauka saura kwana ɗaya rak👌🏻💃🏾_ _Littafaina biyu da nakeyi yanzu haka YAFI ZAMAN AURE da ME YA JAMIN? A baya regular na kowanne 300 ne VIP 600 so yanzu abun ya canza idan ki/ka nason duka biyun regular zakiyi subscribe da ₦400 ne VIP kuma duka biyun zaki biya ₦700 ne wannan ya faru ne sakamakon wani dalili wanda garabasar zata ƙare daga ashirin ga watannan ne so ku hanzarta biyan naku maimakon ₦900 vip 2 books ya koma ₦700 regular 2 books ya koma ₦400 tabbas sai me rabo, saura kwana ɗaya rak👌🏻💃🏾._

_Zaku iya samun damar cigaba da karanta wannan littafai ta hanyar biyan kuɗinku ta 0255526235 Gtbank ko kati MTN ta WhatsApp number 09013718241_
_Yan Niger kuyi mgn ta wannan number domin biyan naku 94775574_

---

Hannunsa ya ɗora saman bakinsa yayi mata nuni da tayi shiru ya fara takowa gabanta yanda yaga gabaɗaya ta firgita shine abinda ya fara burgeshi ya matseta sosai ya rage ɗan taƙi ƙalilan tsakaninsu sannan ya sauke zuciya yace "banason rawar jikin nan ba wani abu zanyi miki ba ki nutsu kin sani kina cika motsawa Salmah zata jiyoki kuma komai zai iya faruwa" jinjina kai tayi cikin razani tace "nasani ka buɗe min na koma ɗakina don Allah...." Hannunsa ya ɗora saman tattausan lips ɗinta yace "zan buɗe miki amma...."
Shammatarta yayi ya haɗe ta da bango ya haɗe tazarar dake tsakaninsu tuni tayi ƙasa a nufinta na durƙushewa ya riƙe weast ɗinta ya kwantar da kanta a jikinsa ya fara ƙoƙarin zame hijjab ɗin na jikinta nanfa ta rushe masa da wani kuka me gunji.....
Da sauri ya jata suka zube a gadon ya ɗauki remote na TV ya kunna ya sanya volume da ɗan ƙarfi yanda zai ɗauke hankali dagajin kukan nata ya kashe glub na ɗakin daidai lkcn data miƙe taja baya a firgice jikinta na karkarwa alamomin tsoro guda 99 duk sun gama bayyana a tattare da ita.

Zare rigar jikinsa yayi ya tsaya a tsakiyar ɗakin yace "idan ya kasance zan rinƙa binki kina guduna kamar wani abin tsoro hakan ka iya fusata zuciyata Kharimatu Ni ba azzalumi bane bazan cutar dake ba Please ki tsaya ba wani abu zanyi miki ba nayi miki alƙawarin bazan kusanceki a wannan yanayin ba kawai ina buƙatar samun nutsuwa da iyalina ne amfanin biyu kenan idan hagu taƙi saika koma dama....."
Da waɗannan kalaman ya hilaceta ya isa gareta ya sanya hannu ya zare hijjab ɗinta tayi saurin sanya hannu ta matse ƙirjinta yabi ilahirin jikinta da kallo yanajin wani yawu yana taruwa a bakinsa yar ɓingilar rigar bacci ce iya gwiwa a jikinta milk da tayiwa choco skin ɗin ta kyau matuƙa hips ɗinta mai faɗi da tudu sun baje a cikin rigar,
Sama yayo da idanunsa ya saukesu saman ƙirjin da taketa rufewa da hannunta yakai hannunsa a hankali ya ɓanɓare nata hannun tudun boobs ɗinta ya caki injin idanunsa ya lumshe tare da

lashe lips ya sake buɗewa ya zubawa nipples dinta masu tudu idanu sun tsaya sunyi wani cako² a cikin rigar kamar zasu zunguri ƙirjinsa

Kukan nata ne ya dawo dashi daga duniyar daya lula ya zubawa smile face nata idanu yaja ajiyar zuciya yace “please stop crying nifa babu abinda zanyi miki da iya nononki zan gamsu Kharimatu idan kika amince nan da ƴan mintina zaki tafi ɗakinki idan kinƙi ki bani haɗin kai kuma zanyi amfani da ƙarfin da Ubangiji ya horemin naci bread na yaga ledar....."

Neman guri tayi ta zauna ta zubawa kayan idanu a haka Mama ta shigo ta ishe ta a zaune ta rafsa uban tagumi tayi murmushi ta zauna tare da dafata ta ɗago firgigit ganin Mama yasata jan numfashi ta cire hannun Mama tace "Banyi tunanin zaki samu kulawa daga Aliyu irin haka ba saboda yanayin izzarsa da kwarjininsa da kuma soyayyar da yakeyiwa matarsa Kharimatu shi namiji da kike ganinsa kamar yaro ƙarami haka yake duk inda yafi samun kulawa nan hankalinsa yafi karkata na fahimci akwai dalilin auren nan naki da Aliyu ya aureki ne domin

wasu dalilansa koda yake dalilansa suna da ƙarfi matuƙar zai kwatanta adalci, nidai fatana Allah ya tsaremin ke"
Ajiyar zuciya ta sauke ta sanya hannunta ta ɗauki wayar daya kawo mata tana dubawa waya ce me tsadar gaske ta girgiza kai tana ƙara bin wayar da kallo iyakar tunaninta bata taɓa kawo ranar da zata riƙe waya me tsadar wannan ba taci naman sosai ita dama masoyiyar kayan sanyi tasha ice cream ta kwanta itadai Mama binta kawai takeyi da kallo tana mamakin irin sanyin da ɗiyar tata tayi duk da dama ita ba ma'abociyar hayaniya bace.

Da dare ne wayar tayi ta ring ta janyota ganin sunansa akan sensor yasa gabanta faɗuwa haka dai tai ƙarfin halin ɗagawa baijata da doguwar mgn ba tambayarta kawai yayi taci abincin tace eh ya kashe, tun daga wannan ranar ya zamewa Aliyu farilla kullum sai yazo gdan ya ganta kafin ya fita aiki wataran idan ya dawo ko kuma yace abashi ita zasuje unguwa ran Mama bayaso saidai bazata iya ce masa a'a ba shida matarsa Granny cema me ƙoƙarin hanawa to itama dole tanada iyaka musamman da yaje yayi mata daɗin baki ya kasheta da kalamai shikenan tayi muƙus a gdan ma idan yazo sai ya kira Anam ɗin sashin Granny ya lallaɓeta da yaudararrun kalamansa ya samu nutsuwa da ita tun tanaƙi har ta saduda.
Satin Salma uku a Niger ta dawo 9ja a lkcn shirye$^{2}$n bikin yayi nisa sosai don har kayan amarya ankai sabon gdan daya gina mata komai Abba ne yayi mata tarkacensu ne na barebari kawai sukayi kayansu duk akaje aka jere a gdan ana jiran sati yazo akai amarya ɗakin mijinta.

Cikin kwanakin da aketa shirye$^{2}$n shagalin bikin ne kuma ɗif ya ɗauke ƙafarsa a gdan nasu babu wanda ya kawo wani abu kowa yabar abin a cewa hidima ce tayi masa yawa Anam ce kawai jikinta yayi sanyi ganin ko waya ya daina kiranta ana saura kwanaki biyu bikin har an fara shagalin biki ana saura kwana uku bikin suka ɗunguma ita da Mama suka koma Guru acan zaaje a ɗaukota ranar da zasu tafin ne ta kira shi a waya kira uku bai ɗaga ba sai a na huɗu ya ɗaga yace ta fito harabar gdan yana jiranta.
Ta zari mayafinta ta fito da zaƙuwa saboda sun kwana biyu basu haɗu ba tun daga nesa ya kafeta da idanunsa kallon kusan faɗuwa yasata daƙyar ta iso gareshi har zuwa lkcn ita yake kallo ta tsugunna tace “Ina yini" numfashi ya sauke ya cire hularsa ya shafa sumarsa yace “kina lfy kinjini shiru amma baki nemeni ba" ƙasa ta sakeyi da kanta cikin kunya tace “nayi tunanin hidima ce ta ɓoyeka" murmushi yayi yace “daba ita ce bafa?" Nuni yayi mata da ta miƙe ta tashi tsaye tana wasa da zara$^{2}$n yatsunta ya kwantar da kansa jikin mota yace “Granny ce tayimin tsakani dake shiyasa na ƙaurace miki"

Da sauri ta kalleshi ya ɗaga hannunsa ya ɗora daidai goshinsa yace “amma kiyi hƙr nasan

zuciyarki ta ayyana miki wasu abubuwan ko? Am kamar me dame ta ayyana miki nasan dai tace miki Aliyu ya gujeki ya daina kiranki ya daina zuwa inda kike, bayan haka sai me?" Dariya tayi da ta bayyana kyawawan Haƙoranta ya zubanta idanu yana murmushi yace "naso ayi komai anan a gama Abba yace a'a saidai ayi a garinku okey ki kasance cikin aminci kiyimin tanadin Pure honey da zaki shayar dani a daren angwancina" turo baki tayi tace "meye ma ya rage bayan komai ka kwashe....." Rufe mata baki yayi yace "Aa bari faɗa ban ɗauki komai ba kawai rage zafi nayi za dai ɗauka zanci na ƙoshi ranar da su Granny bazaa sanyamin idanu ba.

Juyawa tayi zatabar gurin yayi saurin riƙota ya haɗata da jikinsa yace "Da banida wani uzuri tare zamu tafi amma babu komai saura ƙiris" haka ya rinƙa yi mata kalami duk ya kashe mata jiki kafin yace "kinsan me" girgiza masa kai tayi ya matso kusa da ita sosai yace "ina sonki...." Kwasa tayi da gudu tana waiwayensa tana dariya shima yanayi mata dariya baibar gdan ba saida yaga tashin motarsu.
Suna ɗagawa juna hannu cike da shauƙin juna har sukayi nisa sannan ya hƙr tunda motarsu ta tashi yaji gabansa na faɗuwa jikinsa duk ya mutu hakanan ya tsinci kansa cikin kewarta daƙyar yaja motarsa ya nufi gdanta da yasa aketa shiryawa ya zauna a falon ya zubawa manyan hotunan su idanu tsayin lkc ya shagala da kallon hotunan daya sanya akayi musu manya ya kafesu a falon kyawunta sihirtacce ba kowa yake gane tana da kyau ba sai wanda yasan asalin sirrin kyau shi kansa a farko idan Nazeer yana yaba kyawunta musawa yakeyi sai yanzu ya gaskata itaɗin kyakkyawace ta kwatance musamman cikin watanni biyun nan daya gyarata da manya mayuka oily skin nata sai wani ɗaukar idanu sukeyi.

Wayarsa ce ta katse masa tunanin Second wife ya gani a rubuce saman sensor na wayar ya ɗauka da sauri tare da lumshe idanu ya kara a kunnensa kafin yayi mgn yaji hayaniya ta cika masa kunne ya miƙe da sauri tare da cewa "Khamilu ina Kharimatun...." A ɗaya ɓangaren akace "mal ka nutsu mun tsinci wannan wayar ne a cikin wata jaka Allah yasa babu security so muna dubawa sai mukaga wannan number ansa Zaujhnoor shiyasa muka kiraka....." Katseshi yayi da cewa naji malam ina matata kardai kacemin hatsari sukayi ida drivern ina Mama?" Wani ne ya karɓi wayar yace "bazamu tantance komai ba amma dai an ɗaukesu ankasu asibitin Dutse saboda yafi kusa da inda sukayi accident ɗin so ana buƙatar makusantans......"
Bai gama sauraron wayar ba ya fice da gudu ya shiga mota ya fice a gdan cikin tashin hankali shidai bazaice ga yanda akayi yaje Dutse ba sai ganinsa yayi a cikin asibitin yana zuwa ya tarar da Alh Ma'aru a asibitin lkcn suna emergency ana ƙoƙarin ceto rayuwarsu abu da ƙarar kwana an samu nasarar samun rayuwar kowa amma banda ta Mama Yabi Allah ya karɓi rayuwarta a wannan hatsari inda Khamilu ya samu karaya huɗu Ita kuwa Anam doguwar suma da Ɓarin cikin da babu wanda yasan dashi ta samu sai karaya ɗaya a ƙafa.

*Oum Hairan*
[11/6, 7:22 PM] Oum Hairan&Affan: *MYJ29-30 Oum Hairan* Littafina na kuɗi kada ki karanta min baki biya ba don Allah idan kinaso ki biya ta 0255526235 Gtbank ko ki turo hoton katin 300 ta wannan number 09013718241 saiki tura evidance of payment ta number dai ko VTU ta 09031307566

Tashin hankali da ɗimuwar da Aliyu ya kasance a ciki ba kaɗan bace daƙyar da rarrashi Abba yasashi ya nutsu tare da nuna masa hƙr shi ya kama da dauriya saboda Anam a gurinsa kawai ya rage zata samu nutsuwa idan shi bai nutsu ba taya ita zata nutsu?
Da wannan kalaman ya ɗan samu salamar zuci ya zubawa amaryar tasa ido da take cikin halin suma sosai yaji takaicin suɓcewar cikin nasa duk da kasancewar baisan sashi ba a ransa yake raya da yanzu yaransa sun kusa zama huɗu fah rashi biyu sukayi ga rashin surukarsa ga rashin cikinsa, a haka Su Mal Datti kakan Anam sukazo aka tafi da gawar Mama zuwa Kano don tafi kusa domin a sutura ta Aliyu baije ba haka ya wanzu a asibitin sai yammaci liss komai ya ɗan tsagaita sukayi transfer ɗin petiant ɗin zuwa asibitin Mal Aminu Kano aka ɗebe su a Embulance zuwa Kano Granny ke jinyan Anam cike da tausayi da jin ƙai tana tuna kalaman yarinyar a mafi yawan lokuta idan anyi zancen mutuwa takance mata.

Granny nidai fatan da nakeyi kada mutuwa ta ɗauke min Mama tabarni nikaɗai ina Gantali a duniya wlh duk ranar dana buɗi ido naga babu Mamana a gefena tabbas idan nima ajalina bai rigaya ba to kuwa sai an rinƙa haɗamin da addu'a domin tsaf zan iya zaucewa"
Hawaye ta ɗauke a idanunta yau ga ranar da take tsoron zuwa ta iso babu mama Yabi mutuniyar kirki da duniya bata ɗaɗsta da ƙasa ba gashi abin yazo mata a daidai lkcn da tafi buƙatarta fiye da komai, Granny ta Jima tana alhinin wannan rashi kafin ta tashi ta nemi makwanci ta kwanta haka suka wanzu a asibitin wajen kwana huɗu sannan Anam ta fara dawowa hayyacinta.

Ta fara buɗe idonta tana me ambaton sunan Allah  a hankali ta fara sauke idanunta kan mutanen dake zagaye da ita ta jima idanunta akan Aliyu da shima ya kafeta da idonsa da suke cikin farin glass a nutse ta ɗaga hannunta ta miƙa masa ya kama hannun nata ta yunƙura alamu sun nuna masa tashi takeson yi ya ta rintse idanunta tanajin azaba da zugi a hannun nata daya karye ta saki wata yar siririyar ƙara data sanyashi kallonta ta buɗe idonta da hawaye ke ƙoƙarin

gangarowa  a hankali cikin muryar tausayi yace mata “Sannu" daga masa kai tayi tana kallon Granny da taketa matsar hawaye a kasalce tace “Granny meye ya kawo mu nan ina Mama...."

Ƙasa taga Granny tayi da kanta yayinda Aliyu ya fice daga ɗakin da sauri, dukkansu tabisu da kallon rashin fahimta tanabin hannunta da kallo ta zuro ƙafafunta ƙasa ta tashi tsaye tana layi ta nufi Granny ta Kama hannunta tace “Idan zan iya tuna wani abu kamar hatsari mukayi ko Granny please ki faɗa min ina Mama inje inganta ince dai ita bataji ciwo ba?" Rungumeta Granny tayi da Muryar kuka tace “kiyi hƙr Kharimatu duk abinda da Ubangiji ya zartas akan bawa shine daidai tabbas mutuwa batada daɗi musamman ta iyaye Kharimatu muna tayaki alhinin rashin salihar mahaifiyarki Ubangiji yasa lahirarta tafi duniyarta...."
Tun kafin Granny ta ida rufe bakinta sabuwar tashin hankali tayi wankan tsarki ta samu gurbi a ilahirin sassan jikin Anam ta rinƙa kallon Granny kanta na juyawa tana ganin abubuwa hurhuɗu kafin kace meye wannan ta sake zubewa a ƙasa luuuuuu.
Daidai lkcn da Aliyu da likitan suke shigowa suka nufota a guje Aliyu ya tallafota yana kiran sunanta amma ina babu alamun zatayi motsi, ɗagowa yayi ya dubi Granny yace “Fada mata kikayi ko?" Share hawayenta tayi tace “To Gadanga meye amfanin ɓoye mata abinda dole zata sani?" Shiru yayi cike da jin takaicin abinda Granny ta aikata ya ɗagata ya ɗorata a gadon ya kwantar da ita likitan yayi yan aikace[2]nsa ya fita daidai lkcn da Momy ta shigo asibitin suka gaisa da Granny ta tambayeta me jiki ta bata lbrn farkawar ta Hajiya Muniba ta jinjina kai tace “Insha Allahu zata tashi rashin Mahaifiya da ciwo saidai Allah ya bamu ikon yi musu addu'a"

A ranar Anam Bata sake farkawa ba sai kashegari ta tashi lkcn Aliyu bainan sai Granny kaɗai shassheƙar kukanta ne ya ankarar da Granny ta farka ta isa gareta tanayi mata sannu ta ɗago tace “Yanzu shikenan Mama ta tafi ta barni? Shikenan bazan ƙara ganinta ba bazan kuma jin kalamanta ba Granny ta tafi kenan?"
Kama hannunta Granny tayi tace “Haka Allah ya tsara sai hƙr da abinda baka isa ka canza ba Kharimatu kedai kiyita addu'a kuma kiyima mijinki biyayya likitan da ya karɓi Habiba kafin ta rasu yace second 2 kafin rasuwar ta sunanki da mijinki take ambato tana barin wasiccin kada a fasa kaiki gdan mijinki tare da faɗawa likitan ya faɗawa Aliyu ya riƙe ki amana ke har rubuta duk abinda ta faɗa likitan yayi sannan ya sanya mata kalmar shahada tayi ta cika"
Kwantar da kanta tayi jikin Granny tanata kukanta me ban tausayi a haka Abba da Aliyu suazo suka ishesu Abba yace “Assha Kharimatu meye na kukan hƙr ai ya zama dole agun duk wanda irin haka ta sameshi" zama Aliyu yayi kusa da ita ya kamota ta dawo jikinsa ya rinƙa shafa bayanta yana raɗa mata “Sorry Please!" Salma dake tsaye kamar gunki ta haɗiyi takaici iya takaici tayi kamar ta juya saidai kuma ta tuna kalaman Yaya Ameey dole ta haɗiye kishinta ta matsa tace da Kharimatu Sannu ya jiki" a hankali ta ɗago suka dubi juna ta janye a jikin Aliyu cike da kunya da tausayin kai tace “Da....da...sauƙi" taɓe baki Salma tayi ta harari gefen da

surukarta take tace “Allah ya ƙaro afuwa ya jiƙan Mama" duk ɗakin saida suka amsa da Amin banda Granny da Hajiya Muniba da kusan itace Ummul aba'isin zuwan Salma dubiyar har gda taje ta sameta tayi mata tatas tare da nuna mawa Aliyu gangancin da yakeson yayi na rusa gdansa daga tushe wannan tasa yace “Indai batazo ta duba Kharimatu ba to karya dawo ya tarar da ita.

Tana gama dubiyar da batakai zuci ba ta juya zata fita Aliyu ya kirata ta tsaya yace “Ina zaki?" A gajarce tace “Gda" murmushin takaici yayi yace jirani mu tafi" batada zaɓi haka ta dawo ta zauna Hajiya Muniba ta haɗa abinci tabawa Aliyu ya karɓa ya tusa Kharimatu a gaba yana bata da farko ƙinci tayi saida ya rinƙa amfani da hikimomi sannan ta karɓa tana haɗiyarsa kamar magani yanata lallaɓata abinda ya ƙara tunzura zuciyar Salma ta cije leɓe a ranta tana kissima da aikinta yayi yanda sukaso da tuni ba zancen Kharimatu akeyi ba babban baƙin cikinta da akace mata wai Kharimatu har ɓarin cikin  Aliyu tayi to waima yaushe har Aliyun ya zaga har yayi mata cikin? Lallai namiji ɗan babansa ita lissafin ta ma bata yake tun kafin auren yayi mata cikin.
Yini tayi a asibitin tana ƙuncin rai tana haɗiyar takaici tana ganin yanda mijin da yakeyiwa kishi irin na a mutu ko ayi rai yanata lallaɓa wata macen a gabanta bata ƙara ƙuluwa ba sai lkcn da ɗakin ya rage sai su uku can ƙasa taji muryarsa yana cewa da Anam “Meyesa kika ɓoyemin kinada cikina a jikinki har saida ya fita nasan dashi?" Itadai batace komai ba yaja dogon gashinta yace “koda yake kema ba lallai kinsan dashi ba Khary nayi baƙin cikin zubewar cikin nan amma babu komai Insha Allahu da wuri zan sake baki wani ai kinaso ko?"
Idanunta ta sauke kan Salma data sunkuyar da kanta tana danna waya shima ta kalleshi yayi mata murmushi yace “yeah so nake ki ƙarajin sauƙi komai zaiyi saiti" Bazata iya jurewa kalamansa ba hakan yasata miƙewa ta saɓi jakarta tace “ƴaƴana sun kusa dawowa daga school mal zan wucce" miƙewa yayi yana kissing hannun Kharimatu yace “Zan shigo anjima ki kulamin da kanki"

[11/6, 7:22 PM] Oum Hairan&Affan: *MYJ31-32 Oum Hairan* Littafina na kuɗi kada ki karanta min baki biya ba don Allah idan kinaso ki biya ta 0255526235 Gtbank ko ki turo hoton katin 300 ta wannan number 09013718241 saiki tura evidance of payment ta number dai ko VTU ta 0931307566

Wani Mugun kallo da Salma ta watsawa Kharimatu saida hanjin cikinta ya kaɗa tayi saurin sunkuyar da kanta inda ita kuma ta fice daga ɗakin ya lura kowanensu da saƙo a zuciyarsa so bayason ɓatawa kansa lkc akan abinda bashi da muhimmanci hakan yasa ya rufawa Salma baya tana tsaye jikin motar sai girgizar bala'i takeyi ya kalleta ya watsar ya shiga yayima motar

key ganin alamun zai iya tafiya yabarta yasata shiga ta rufo ƙofar da ƙarfi ya kalleta ya watsar ya ja motar ya bar harabar asibitin.
Sunyi nisa sosai taji bazata iya haɗiye abinda kecin zuciyarta ba tace “Me yasa kakeson zubar da ƙimarka da darajarka gurin yarinyar nan ne Aliyu kai ko kunya bakaji jibi yanda kake wani zaƙewa tana jisgaka....."
Kallonta yayi da gefen ido yace “kunya? Zubar da ƙima?" Kuma a matata ta sunnah waɗannan kalaman suka samu gurbi? Hmmm!" Daga haka yaja bakinsa yayi shiru itama ta tsuke nata bakin badon ta rasa abin cewa ba sai don batason kalamanta suyi yawan da zai fahimci tuban muzuru tayi masa.

Har suka isa gida babu wanda ya sakewa kowa mgn sun jima a wannan yanayin shiyasa abin bai wani dsmunsa ya haye sama ya fara ayyukan dake gabansa bayan ya kammala ya fito ɗaure da towel tana zaune a parlourn ta rafsa tagumi ya matsa gabanta ya sanya hannu ya cire mata tagumin tayi firgigit kamar wacce ta tashi a bacci ta dubeshi yayi mata murmushinsa me sanyata ƙara jin kishinsa yace “Meye yaja kike sanya kanki cikin damuwa ne akan abinda ubangiji ya hukunta Salma kinsan ita ƙaddara tana zuwarwa mutum ne batare da ya shirya mata ba abin buƙatar kawai ka zama mumini na ƙwarai wajen karɓar ta a duk yanayin data faɗo maka mi kyau ko akasinta, bare a aurena da Kharimatu banga abinda zaisa ki damu ba kinsanta kinsan wacece ita batada matsala kusan kece kika raineta so meye damuwarki?"

Ajiye zuciya tayi ta janye kuncinta daga hannunsa ta miƙe ta nufi kitchen yabi bayanta da kallo ya rasa wanne irin mugun kishi ke addabar zuciyar Salma da har yake neman taɓa muhibbar aurenta"
Taɓe baki yayi ya miƙe ya koma ɗakinsa ya dauki doguwar riga yasa ya

fito da key na mota a hannunsa tana tsaye jikin window taji bude ƙofar tasa ta juya ta zubansa ido wani tuƙuki nayi mata zillo a zuciya tunda ta tsaya tunanin ta inda zata ɓullowá wannan baƙon lamari daya faɗo rayuwarta takeyi. batare data shiryawa furuci ba ya kufce mata tace “Aliyu...." Tsayawa yayi yana gyara kwalar rigarsa tace “Ina zaka?" Cikin dakiya ya juyo ya dubeta ya ɗan saki mata fuska yace “zanje nagano jikin Kharimatu ne" ganin yanda yanayin fuskarta ya sauya yasan mgnr ta daketa batare da yayi zaton cewarta ba yaji tace “Ina buƙatar Ikcnka inason muyi wata mgn dakai idan ka dawo ka gaisheta kace nace inayi mata sannu" ta faɗa a ƙarshen furucin nata tana aro murmushin yake tanayi masa. Bin ta yakeyi da kallon mamaki da sallamawa yace “Ok ba daɗewa zanyi ba"
Yana faɗin haka yasakai ya fice ta taune leɓe cike da ƙunar zuciya ta zauna daɓar bisa kujerar tana lalubar number Ameey ta ɗaga tana cewa “sarkin ƙorafi yau da wanne akazo?"

Tattara numfashinta tayi ta ajiyeshi waje guda tace “Idan naci gaba da bin shawararki zuciyata bugawa zatayi Yaya Amina mijina ya wucce tunaninki akan yarinyar nan nifa na fara zargin basubar ƙasa haka ba sunbi ta ƙarƙashinta wajen siye zuciyarsa yau da bakiga yanda ya rinƙa yi mata a gabana ba ko kunyar ganin idona baiji halan Malamin nan bai fara aikin bane har yanzu?"
Murmushi Ameey tayi tace “Kin cika gajen hƙr ke yanzu zakice baki fara ganin tasirin aikinmu ba kina gani fah Mal cewa yayi muddin uwar Kishiyarki na raye duk wani sihiri da za'ayi mata bazai yi tasiri ba nice na koma nace masa a kawar da uwar gashi har anyi an gama yanzu kuma nasa akeyin aiki akan ya haɗeku guri guda ta yanda zamufi samun damar aiwatar da abubuwa"
Girgiza kai tayi tace “Nifa bangano alkhairi a zamana gda ɗaya da wannan yarinyar ba zuciyata bazata ɗauka ba" “Aikuwa dole ki ɗauka muddin kinason kiyi nasara" cewar Ameey taci gaba da cewa “idan kika lallaɓashi tare da nuna masa amaryarsa tana buƙatar kulawa da tattali duba da rashin Mahaifiya da tayi da kuma lalurar dake tattare da ita kisan dai yanda zakiyi da salo da hikima ya amince ya haɗaku idan ya amince da hadekun ki sanar dani zan sanar da Mal ka iya zai turo baƙaƙen aljanu suyi biso a ɗakin nata muddin wannan abun yana ɗakinta ita da zama lfy har abada zasuyita bata kashi har sai ta gudu da ƙafafunta idan kuwa bata gudu ba to tabbas zasu kasheta kamar yanda suka yiwa  Zuhrah Kishiyar Janah ƙawata kedai ki zuba ido kiyi kallo kuma ki koyi kirsar ɓoye kishinki ga mijinki gareta domin muddin kika ɓata takun aiki zai lalace"

Daɗi matuƙa Salma taji da mugun tanadin da Yayar tata take shiryawa kishiyar Tata hakan yasata wani tsallen murna tace “Shiyasa nake matuƙar ƙaunarki My sis ki daɗe kiyi ƙarko Indai dake bamayin kukan baƙin ciki amma fah dole mu iya taku kinsan Hajiya kullum wai wata nasiha takemin wai naji tsoron Allah koda tsoronta nakeji" dariya suka sheƙe da ita Ameey tace “Manta da tsohuwar nan ita kullum bata ganewa aini nuna mata nake nafi Shaikh Sudais tsoron Allah"
Dariya suka kumayi tare da sallama ta aje wayar ta miƙe ta nufi kitchen ya ɗauko juice da cake ta dawo ta zauna tanaci tana latsa wayar zuciyace ta raya mata ta fara aikinta tun yanzu hakan ya bata ƙwarin gwiwar kiran wayar Aliyu ya daga tace “Baby ya jikin Sis?" Kallon Anam yayi yace  “Tanajin sauƙi kinganta tanata shagwaɓa bacci ma takeji"
[11/6, 7:22 PM] Oum Hairan&Affan: *MYJ33-34 Oum Hairan* Littafina na kuɗi kada ki karanta min baki biya ba don Allah idan kinaso ki biya ta 0255526235 Gtbank ko ki turo hoton katin 300 ta wannan number 09013718241 saiki tura evidance of payment ta number dai ko VTU ta 0931307566

Haɗiye abinda ke damun zuciyarta tayi ta harari gefe tace “Uhm madalla ka gaisheta aje wayar tayi shima ya aje suna kallon juna yace “ki daina zama da yunwa banason zama da yunwa Khary" lumshe idonta tayi ta buɗe yace “Ok bazaki daina ɗinba kenan" ƙasa tayi da kanta tana wasa da hannunta ya riƙo zara$^2$n yatsunta da sukasha lalle ya lumshe idonsa yace “lallai nan yayimin kyau" ɗagowa sukayi tare ya zuba idanunsa cikin nata yace “likita yace gobe zai sallameki kinji sauƙi am idan an sallameki gdanki zan kaiki" da sauri ta dubeshi ya ɗaga mata gira yace “hakan ya kamata zaman nan naki a gda bazai yiwu ba gara kije gdanki kema ki samu ladan aure kamar kowacce mace"

Girgiza masa kai tayi ya sanya hannu ya ɗago fuskarta yace “idan kika koma gdanki zakifi samun nutsuwa" bata iya jayayya ba hakan yasata yi masa shiru yayi murmushi yace “shiyasa nakesonki" ya ɓata lkc a asibitin kafin sukayi sallama da Granny ya tafi tunda yaje gda Salma ta kawo masa abinci ta zauna kusa dashi tana wasa da yatsunsa yana cin abincin suna hirarsu tana dariyar yaƙe saida taja hankalinsa sosai sannan ta ɗago ta dubeshi tace “My Haidar!" Dubanta yayi tare da tattara hankalinsa waje guda yace “yadai My Salmah

Sunkuyar da kanta ƙasa tayi tace “Da zakayimin wannan alfarmar da zanji daɗi sosai Aliyu nayi alƙawarin duk wani abu da kake tsoro bazai faru ba don Allah ka amince dani" aje cokalin yayi ya zubanta ido tare da cewa “Wanne Alfarma kenan?" Sosa kanta tayi tace “Kada ka raba mana gda da Kharimatu saboda yarannan kaga Ni ina zuwa aiki kuma ina yawan tafiye$^2$ idan tana gdan zasu zauna tare tunda dama sun saba rainonta ne kuma kaga nan yafi kusa da makarantarsu fiye da can inda kake gini bayan haka kaima sauƙin ka ne komai katashi siye ɗaya zaka siya na amfanin gda memakon idan ka rabamu da komai saika nemi biyu sannan inason mu samu kusanci kamar yanda Hajiyata da Hajiya ƙarama suke inason mu zama abu ɗaya ta yanda zakayi alfahari damu, Amma fah kada ka canza min fassara iyakar gskyta kenan" Tana mgnr tana cigaba da wasa da yatsunsa.

Zubanta idanu yayi a hankali yakai hannu ya ɗago fuskarta ta lumshe idanunta tare da shigewa jikinsa shikuma ya matseta cike da so yace “Meye ya canzamin ke kikayi laushi haka ne My Salmah naga a farko kin ɗauki abin da zafi yanzun kuma kin sauka da wuri" murmushin bakada wayo tayi masa tace “tausayin Kharimatu ne ya fara canzamin tunani sai kuma nasihar Hajiyata Aliyu na gane abinda kake nufi kaine ka cancanci riƙe maraicin Kharimatu shiyasa naji a raina zan taimaka maka na tayaka riƙon amanar nan musamman da akace Mahaifiyarta kafin ta rasu ta damƙa maka ita amana"

Sosai Aliyu yaji daɗin kalaman matarsa nan take yayi mata alƙawarin haɗa su gda ɗaya da Kharimatu suka tashi sukaje suka kwanta washegari tun safe yasa aka gyara masa daya bangaren na gdan dake dama gdan nasa yanada girma akwai ɓangare ɗaki biyu manya da parlour da toilet a kowanne ɗaki sai kitchen ƙarami batare da ya sanar da kowa abinda suka shirya ba yasa aka ɗebo kayanta da aka shirya a sabon gdan aka dawo dasu nan masu shirya gidaje suka baje fasahar su wajen tsara mata sashin duk da cewar kayan sun yima ɓangaren yawa haka aka shiryasu aka zuba mata wasu a store da yake Alh Ma'aru ya narka mata kuɗi sosai a wancan gdan.
Kwana uku ta ƙara aka sallameta a asibiti da farko sunso tafiya da ita gda suci gaba da kula da ita saidai basu samu wannan damar daga mijinta ba yayi kicin$^{2}$n ya matse lamba kan saidai abashi matarsa shi ya gaji da wannan galantoyin hakanan da Granny ta fusata tace “ga matarka nan idan ka tafi da ita kasa mata mai da yaji ka cinye ƙarewar so sakarai kawai"
Baiji haushi ba ta fice driver ya ɗauketa shima ya haɗa musu kayansu sai gda tunda suka taho take hawaye har sukazo ƙofar get na gdan yayi horn ta ɗago gabanta yayi muguwar faɗuwa ganin gdan da ya kawota ta dubeshi cikin kaɗuwa tace “Daddyn Farooq gdan Aunty Salma ka kawoni fah" shafa sumarsa yayi ya ɗaga mata gira yace “Gdan Aliyu dai ko Kharimatu tunda Salma batazo dashi a gara ba" numfashi ta sauke yana matsowa jikinta tace “Amma ai ba anan zan zauna ba kace dasu Granny" murmushi ya sake yi mata ya tallafi kuncinta ya ɗora bakinsa saman nata ya lashi lips ɗin ta da harshensa ya ɗago yace “Zanfi samun nutsuwa idan kuna a guri ɗaya kada ki tashi hankalinki bazaki samu matsala da Salma ba ta sauko sosai kinji My Khary"

Ƙasa tayi da kanta cikin zullumi zuciyarta na bugawa da ƙarfi taji ya buɗe motar ya fito ya buɗe mata ta zuro ƙafafunta cikin fargaba yayi gaba tana binsa a baya kamar mara gaskiya ya buɗe falon suka shiga da sallamarsa Salma dake zaune ta miƙe Kharimatu tayi saurin raɓewa a jikinsa domin mugun tsoron Salma takeji abinda yaja sukayi dariya su biyun Aliyu ya shafa bayan Kharimatu yace “My Salma kin tsoratamin mata da yawa" dariya tayi tace “Double sorry Ƙanwata ki daina jin tsorona babu abinda zanyi miki kinji" hannu tasa ta janyeta a jikinsa ta kama hannunta tana mata murmushi suka haura saman.

Ta buɗe mata ƙofar shiga sashin ta yana biye dasu a baya saida ta shigar da ita har cikin bedroom ɗinta ta zaunar da ita a gefen gado tace “amarya kike sak yau gaki a angonki ina fatan hannun bazai hana ku sakewa ba?" A mugun  kunyace da al'ajabin canjin na Salma tayi ƙasa da kanta Aliyu dake tsaye yana mamakin yanda matar tasa ta sauko cikin ƙanƙanin lkc yace “sai abishi a hankali ai kinsanni da tausayi" juyowa tayi ta sakar masa murmushi tace nasan

wannan yanzu meye zakuci a sama muku?"
Agogo ya duba takwas da minti biyar na dare ya ɗago yace "na hutassheki kema kije ki kwanta ki kulamin da kanki zan fita na samo abinda zamu tari baƙuwar tamu" lumshe idonta tayi tace "Idan kayi hakan zanji daɗi kaje ka dawo zan tayata hira har ka dawo" jinjina kai yayi ya juya ya fice ta zauna kusa da Anam tana kallonta tana saƙa abubuwa da yawa a ranta tana murmushin da ita kaɗai tasan ma'anarsa haka suka zauna jefi² tana yima Anam hira itadai saidai tayi ajiyar zuciya domin kuwa zuciyar Tata a karye take kukan ne kawai batason tabashi damar zuwa.
Sun jima a zaune Kharimatu har ta farajin bacci sukaji shigowarsa ya buɗe ƙofar ya shigo da sallamarsa ya aje ledojin ya fara ƙoƙarin cire rigarsa yace "Am My Salmah ki ɗauki leda biyu ki tafi dashi na gde da kulawa Allah yabarni daku a haka" miƙewa tayi ta ɗauka tayi musu sallama daƙyar ta haɗiye abinda yake cakar zuciyarta ta shiga ɗakinta ta kulle tayi jifa da ledar hannun nata ta zube a jikin ƙofar ta ɗora hannunta akanta zata kurma ihu tayi saurin toshe bakinta taja ɗuwawu ta isa jikin gadon ta haɗe kanta da gadon ta saki kuka.

Zama yayi kusa da Kharimatu ya kamo hannunta da hannunsa yakai bakinsa yayi kissing nata yaja fasali yace "ya kikeji a zuciyarki game da wannan sauyin da aka samu a gurin Auntynki?" Ɗago manyan idanunta tayi ta saukesu akansa baisan meye yasa ba baya jure su haɗa ido da yarinyar mugun kwarjinin takeyi masa hakan yasa ya sauke idonsa yace "kiyi mgn" ajiyar zuciya tayi ta yunƙura zata miƙe ya janyota ta faɗo jikinsa yakai hannu ya riƙe hannunta me ciwon ya saita fuskarsa a tata tare da haɗe bakinsu guri ɗaya suka lumshe ido a tare duk da a mugun tsorace take dashi haka ya rinƙa sarrafata bai ƙyaleta ba saida ya samu nutsuwa da ita sosai ya shafa saman goshinta yace "kina da baiwa My Kharry Allah yayi miki albarka" itadai kunyarsa takeji sosai duk da ba wannan ne karo na farko da hakan take faruwa tsakaninsu ba inda sabo ma kusan ta saba dashi a cikin watannin auren nasu baya bata da sauƙi.
Bayan komai ya nutsa ne sunyi wanka ya buɗe musu abinda ya siyo sukaci dakansa ya rinƙa bata a baki sukaci sukayi hani'an sannan sukayi brush Suka sake kwanciya, saime cikin dare kamar wacce aka tsikarawa allura ta zabura ta miƙe cikin wani irin tashin hankali tana furta "A'uzubillahi minasshaiɗanur rajim Innanillahi wa Innah Ilaihirraji'un" shima tashi yayi a firgice ya riƙeta da ƙarfi yana kiran sunanta ta ƙanƙameshi jikinta yana wata muguwar tsuma ƙirjinta sai bugawa yakeyi da ƙarfi.

[11/6, 7:22 PM] Oum Hairan&Affan: *MYJ35-36 Oum Hairan* Littafina na kuɗi kada ki karanta min baki biya ba don Allah idan kinaso ki biya ta 0255526235 Gtbank ko ki turo hoton katin 300 ta wannan number 09013718241 saiki tura evidance of payment ta number dai ko VTU ta 0931307566

Kiran sunanta yayi da ƙarfi yana cewa "Me... Meye ya firgitaki haka meye damuwarki" sake

shigewa tayi jikinsa tanajan ajiyar zuciya ganin yanda ta fice a hayyaci Ikc guda yasashi fara tofa mata ayatul kursiyyu a tsakiyar kanta da addu'o'in neman tsari a hankali yaji zufa yana keto mata zuwa anjima kuma yaji taja fasali ya nitsa hannunsa cikin sumarta yace “Meye ya tsorataki haka My Khary?" Numfashi ta sauke ta ɗago ƙwayar idanunta da suke cike da bacci ta sauke akan fuskarsa ta sake jan fasali ta kwantar da kanta a ƙirjinsa tace “Wasu irin halittu ne masu kama da gizo² suka biyoni suka ɗafemin jikina suna cizona kuma duk inda suka cijeni rami yakeyi shine inata neman taimakonka kawai kayi tafiyarka ka ƙyaleni a tsakiyarsu inata kiranka kaƙi juyowa"
Shafa bayanta yayi yace sharrin mafarki ne kawai shine kika tashi kina ihu salon ki tashi mutanen gidan oya koma mu kwanta saida safe"  komawa sukayi suka kwanta ta sake sabuwar addu'a bacci ya ɗauke ta tana maƙale a ƙirjinsa shikam hakanan yaji zuciyarsa taƙi kwanciya da labarin mafarkinta data bashi koda yaga tayi bacci saida ya sake tofeta da addu'a sannan shima yayi baccin.

Da asuba ita ta tasheshi yajasu sallah suka sake kwanciya ya maƙaleta batason yanda yake nuna mata nacinsa saidai bazata iya hanashi haƙƙinsa ba haka suka bawa juna aikin safe suka sake sabon bacci sai goma sukaji ana taɓa ƙofar ta miƙe da sauri ta faɗa bathroom shine ya tashi ya buɗe ƙofar yana miƙa Salma ta leƙo ɗakin tans cewa “Ina sister na kaida baka gajiya da bacci ka makarar da ita koda yake yau Sartuday ku huta abinku"
Lumshe idanunsa yayi yace “Tana bayi yanzun zata fito" yana mata bayani idanunta nakan gadon da suka turmushe da kuma bra ɗin da take ƙasa wani mashi ya caki ƙirjinta ta haɗiye wani yawu me ɗaci ta dubeshi tace “ok idan kun shirya ga breakfast can a dinning" jinjina kai yayi ta juya ta fice ya koma ya ɗebe kayan daidai Ikcn data fito a wankan tana goge sumarta ya zagaya ya rungumeta ta baya yayi kissing wuyanta yace “Morning My Chocolate" murmushi Kalmar tasata.

Ta janye a jikinsa tace “kayi wanka tukunnan" nufar bathroom ɗin yayi yana cewa “kamata yayi kiyimin wankan nan ba kibani umarnin yin wankan ba" shiru tayi masa ta buɗe wardrobe ta ɗauki kayanta wasu sabbin riga da zani na atamfa tasa ta ɗaura ɗankwalin tana sanya ɗan kunne ya fito ya karɓa ya saka mata ya miƙa mata mai ya kashe mata idanu tare da nuna mata jikinsa inda sabo ta fara sabawa da sangartarsa ko Ikcn da yake ɗaukar ta yakaita hotel idan yayi wanka miƙe mata yake yace ta shafa masa hakan yasa ta saba ta shafesa tsaf ta ɗauko masa kayansa data gani a gurin ta taimaka masa yasa ya kamo hannunta suka fito.

Salma na zaune ta zuba uban tagumi a parlourn taji saukowarsu tayi saurin kawar da damuwarta tana mamakin yanda taga Kharimatun Ify ƙlau nandanan taji wani baƙin ciki ya cushe mata zuciya wannan wacce irin yarinya ce duk abinda aka shirya mata yake neman watsawa a banza, ƙwafa tayi a zuciyarta tace “in kinsan wata ai bakisan wata ba zanyi maganinki bari muga kamun ludayin wannan da akace nasa miki a abincin tukunna" zama sukayi a dinning ɗin ta gaisheta cikin ladabi ta amsa da murmushin da baikai zuci ba da kanta ta haɗawa kowa break ɗin Kharimatu ta ɗauki nata a kunyace tayi bismilla takai bakinta nandanan annurin fuskar Salma ya ɗauke jin tayi bismilla abincin da bata iya ci ba kenan komanta ya rushe duk kuɗin data kashe sun tashi a banza wannan shegiyar yarinyar dole a canza taku ƙaramin asiri bazai kaita ƙasa ba saidai tsafi.
Daƙyar Salma ta rinƙa tura abincin bayan sun gama ta tashi ta kwashe kayan Kharimatu ta miƙe domin ta tayata tace “aa yi zamanki ki huta amarya bata wahala kedai ki kula mana da mijinmu shine kawai aikinki" kunya ce tasa Kharimatu ƙasa da kanta ya riƙo hannunta yace “kinji abinda akace miki ko ki kula dani" yanda yayi mgnr yabasu dariya sukayi dariya ya miƙe yace “Zanje na gaida su Hajiya ku kulamin da kanku" fatan alkhairi sukayi masa Kharimatu ta miƙe ta sake gyara parlourn suka zauna suna hirarsu sama sama Salma ke janta da hirar nandanan ta saki jikinta sukayita harkokinsu tare ranar har girki tare sukayi abinsu can yamma aka dawo musu da yaran gdan da suka tafi hutu gdan kakanninsu yaran suna ganinta suka fara murna ta jasu jikinta sukayita shirmensu a haka Aliyu ya dawo ya tarar dasu yaransa sai nishaɗi sukeyi da ganin Uwar goyonsu shima sai yajishi cikin farin ciki ya zauna a cikinsu yana tayasu Salma sai tsiya takeyi masa wai yamai da kansa yaro.

Basu suka bar parlourn ba sai goma saura na dare Muwaddat tace “Aunty yau ɗakinki zan kwana" Farooq ma yace “nima acan zan kwana" Aliyu dake zaune ya miƙe yace “Nima Aunty yau a ɗakinki zan kwana" dariya sukayi Salma tace “aikuwa saidai kai ka hƙr kabarwa yara Auntynsu" murmushi yayi yace “dake don yara aka halicce ta ba to aikuwa saidai su su hƙr subarmin so nake na samo musu ƙani da wuri" haɗiye takaicinta tayi ta nufi saman tana cewa Allah ya taimaka zanyi murna da hakan mukam munyi adabo da haihuwa" ɗaukar Jannat tayi tace “muje mu kwanta saida safe ko" miƙewa dukansu sukayi suka bita suna murna yau zasu kwana da Auntynsu. Muryar Aliyu taji a bayanta yace “My Kharry!" Tsayawa tayi ya tako ya dafata yace “ina jiranki a ɗakina" saida ƙirjinta ya buga tayi ƙarfin halin cewa ok bari na kwantar dasu"

Jinjina mata kai yayi ta nufi saman yana biye da ita ta buɗe ɗakin yaran ta kwantar dasu tare dayi musu addu'a bayan tasa musu kayan baccinsu kwanciya tayi a gefen su sunata yi mata surutu har bacci ya ɗauke su Dukansu.
Shirun Aliyu yaji tayi yawa ya miƙe ya buɗe ƙofar ya nufi ɗakin yaran ya isheta tana bacci

rungume da Jannat ya zubanta ido shauƙin ƙaunarta da sha'awarta suna ɗibansa ya matsa ya zare Jannat ɗin ya kwantar da ita ya ɗagota gabadayanta ya nufi ɗakinsa da ita ya kwantarta kamar wata baby yana ƙare mata kallo yaja numfashi ya ɗora bakinsa saman lips ɗinta ta buɗe idanunta akansa shima ita yake kallo tace “ina yaran?" Dariya tambayar tabashi ya janye yace “da kina tunanin kinci bulus ne zaki tafi gurin yara kibarni shanye kamar mayafi" miƙa tayi ta tashi zanne ya zauna a gefenta yace “meye na miƙewar?" Murza idanunta tayi tace “kayan nan zan cire" janyota jikinsa yayi yace “ki kwanta abinki zan cire miki" hannu yakai bayanta ya zuge zip ɗin ya zuge na sikelt ɗin ya zare mata ya ɗora bakinsa saman wuyanta yana lasa ta lumshe idonta tanajin wata muguwar faɗuwar gaba da batasan meye ya sabbabata ba cikin lkc ƙanƙani kanta yayi wata muguwar sarawa ta sanya hannunta biyu ta riƙe kanta ta saki wata razannanniyar ƙara data sanya kowa na gdan fitowa...........

Oum Hairan
[11/6, 7:22 PM] Oum Hairan&Affan: *MYJ37-38 Oum Hairan* Littafina na kuɗi kada ki karanta min baki biya ba don Allah idan kinaso ki biya ta 0255526235 Gtbank ko ki turo hoton katin 300 ta wannan number 09013718241 saiki tura evidance of payment ta number dai ko VTU ta 0931307566

Ƙoƙarin riƙeta Aliyu yakeyi saidai tafi ƙarfinsa watsoshi tayi ƙasa itama ta zube tana wani irin abu daya tashi hankalinsa ya matsa ya riƙe ta daidai lkcn da Salmah ta turo ƙofar ta shigo tayi kansu da sauri tana faɗin subhanallah meye ya sameta?" Kallonta kawai Aliyu yayi yaci gaba da yima Kharimatu addu'a amma kamar Bama yi yakeyi ba ganin abin bana wasa bane ya tashi ya fita yana kiran wayar Alh Ma'aru dake dare baiyi nisa ba ya sameshi nan yake faɗa masa abinda yake faruwa hankalinsa ya tashi matuƙa  da kansa ya fita ya ɗauko limamin unguwarsu suka nufo gdan nasu bayan ya ɗauki Granny yanayin da suka tarar da ita ya basu tsoro liman ɗin ne ya soma yi mata addu'a ta rinƙa miƙewa tana son ƙwacewa daƙyar Suka samu ta fara mgn cikin wata irin murya data tsorata kowa dake gurin sukaji ta fashe da kuka tana cewa “mu ku ƙyalemu bamu muka kawo kanmu ba ita ta taɓomu mu haukatata ko mu sanya mata ciwo mun kasa yin ko ɗaya sharaɗin zuwanmu bazamu barta ta samu ciki ba amma abin takaicin saida ciki ya shigeta" wata dariya ta ƙara fashewa da ita  data sanya Salma matsawa taci gaba da soki burutsun surutunta liman nata kwarara mata karatu.

Basu suka samu ta jirge ba sai wajen asuba sannan ta kama bacci liman ya sharce gumi ya dubi Aliyu yace “ka biyoni gda ka karɓo mata rubutu gdy yayi suka fita suka barta kwance

tanata baccinta suna fita Salma ta sheƙe da dariya  ta matsa kusa da gadon tace “yaro man kaza kin tabka kuskure da kika bari kika shigo gonata zaki gane kurenki mijina gdana sunfi ƙarfinki sai na mayar dake abar tausayi kuma abar kwatance a duniyar maciya amana" tsaki taja   ta juya ta fice daga ɗakin bai jima sosai ba ya dawo kamar yanda Mal Kabir ya faɗa masa. Haka ya rinƙa shafa mata rubutun a ƙasan mararta zuwa ƙirjinta ta rinƙa sakin ajiyar zuciya bai jima da gama shafa mata ba ta buɗe idonta ta saukeshi a saman agogo takwas da rabi ta yunƙura zata miƙe ya ɗagata taja numfashi tare da sauke idanunta akansa yayi mata murmushi yace “Ya jikin" lumshe idonta tayi kanta har yanzu sarawa yakeyi ta buɗe idonta akansa tace “Meyesa baka tasheni da asuba ba?" Kawar dakai yayi yace “bakida Ify ne shiyasa" da wannan ta miƙe ta shiga bathroom tayi wanka ta ɗauro alwala tayi sallah ta shirya cikin wasu riga da sikert na jeans tayi kyau sosai sauka yayi ƙasa ya ɗauko mata break ya dawo.

Zama sukayi da kansa ya rinƙa bata abincin a baki tun daga wannan rana ya zame mata al'ada duk dare basa bacci kwana yakeyi akanta sai safiya tayi suke samun nutsuwa tsayin wata guda sai kuma laulayi ya sawo kai kullum tana kwance kamar ruwa tun ga amai da take fama dashi babban abinda ya fara bata mamaki da tsoratata a yanayin zaman gdan nasu idan yana gda Salma zata nuna mata tafi kowa kulawa da ita idan bayanan kuwa ko leƙota batayi haka suke rayuwa sannu a hankali Ikc ya rinƙa tafiya cikin yanada watanni hudu cikin wani dare da bata mantawa dashi ranar ba ita keda girki ba Salma ce tun yamma takejin yanayin zazzaɓi ajikinta haka ta gama abinda takeyi a daddafe ta kwanta bacci ya ɗauketa cikin baccin taji wani mugun huci yana tunkarota ta buɗe idonta da sauri tare da dirowa a gadon daidai Ikcn da wata doguwar halitta ta ƙaraso gabanta batayi aune ba taji an feso mata wani abu me azabar raɗaɗi a jikinta azabar data ratsa ta itace tasata sakin wata gigitacciyar ƙara ta zube a gurin kasancewar dakin a kulle yake Tsakanin ɗakinta dana Aliyu akwai tazara baijita ba amma Salma taji ta basar hakanan tayita juyi tana murƙususun azaba ta daɗe sannan ta samu raɗaɗin ya ragu tana addu'a sannan ta buɗe idanunta taga wannan mutumin ya ɓace taja ajiyar zuciya tanabin jikinta da kallo.

Me zata gani wasu irin ƙananun ƙuraje ne gabaɗaya jikinta sai zubar da ruwa sukeyi aikuwa ta mike a razani tana ƙara bin jikin da kallo tana faɗin “Innanillahi wa Innah Ilaihirraji'un" tsoro ya sake kamata ta tsigar jikinta tana tashi wasu zafafan hawaye suka zubo mata cikin tashin hankalin da bata taɓa shigaba tace “Na shiga uku Ni Kharimatu wannan wacce irin masifa ce?" Ashe wasa farin girki ne cikin Ikc ƙanƙani taji kanta da jijiyoyin jikinta sun ɗaure ɗam ta kasa ko matsa komanta kafin kace meye wannan ta yanke jiki ta faɗi.
Bata farka ba sai a gadon asibiti tana buɗe idonta jikinta ta fara kallo ta rintse idonta cikin ƙyanƙyami da tashin hankali ta rushe da wani kuka me gunji tace Innanillahi Granny meye wannan a jikina" Granny da Mom da suke zaune a gefe suka nufota da sauri cikin tsananin

tausayi Granny tace “Sannu Kharimatu ke kuma taki ƙaddarar kenan daga wannan sai wannan Ni waɗannan ƙuraje don dai sun dage akan ayi maganin asibiti ne nikam nafi tunanin sihiri ne" Mom ce ta cafe da cewa ashe muna ɗaya dake lamarin yarinyar nan akwai alamun bincike Hajiya iyakar zamanmu da ita batada jinnu kina gani fah dagayin aurennnan abu yaƙi daɗi kullum ita kenan ta yanke jiki ta faɗi yanzu kuma ga wata sabuwar masifar ta sako kai kiga fa jikinta yanda ƙurajen nan suka girma fata me kyau ta zama kamar bayan bishiya sai daddarewa takeyi"

Jinjina kai Granny tayi tace “Ma'aruf ne yake biyewa yaron nan Ni dama Muniba tun farko banso zaman Kharimatu da Salma guri ɗaya ba nasan sai an cutar da yarinyar nan" karɓa Mom tayi da cewa “ai gashinan sun fara gani Hajiya dole idan yarinyar nan ta samu sauƙi ya raba musu gda ko kuma ya sawwaƙe mata tunda zamansu taren ba dole bane" akan wannan shawarar suka tsaya.
Tun ranar data farka a asibitin take sanya idon ganin Aliyu shiru babu shi babu labarinsa har yau gashi kwana uku da farkawarta abinda yake bata mamaki ko a waya bataji yana kiran Granny ba yau tun safe ta tashi jikinta sai ruwan mugunya yake zubarwa abinda ya tashi hankalin kowa babu shiri Granny ta Kira Aliyu ta sanar dashi abin mamaki sai cewa yayi da ita shifa ayi duk abinda ya dace Bama ya gari yana Lagos  zai turo musu da kuɗi" jinjina kai Granny tayi tace “Anya Aliyu yau yarinyar nan watanta guda a asibitin nan tun washegarin ranar da aka kawota baka ƙara dawowa ba matarka ma batazo ba meye yake faruwa ne haka?"

A kausashe yace “Itama batanan muna tare anan yaran suna gdansu Salma daganan Dubai ma zamu wucce Salma keda ciki zataje ta huta acan maybe sai yakai 6 months zamu dawo" murmushi Granny tayi tace “Lallai ne Gadanga kabar yarinya marainiyar Allah cikin lalura ka ɗauki matarka kunbar gari kuma har kana sanar da cewa zaku wucce Dubai to ita ame kabarta da nata cikin?"
Tsaki yayi yace “Ke wlh Granny da son takurawa kike naga gashinan kuna kula da ita" bazata iya jure lamarin ba wannan tasa ta kashe wayarta takai dubanta ga Kharimatu da takejin duk abinda yake faruwa tace “Inason ganinsa Granny kice yazo don Allah" hawayen tausayinta Granny ta share tace “zaizo Kharimatu wani aikine na gaggawa ya taso masa ya tafi Lagos amma kina ransa kiyi hƙr kinji kiyi fatan Allah ya baki lfyrki kawai"
Komawa tayi ta kwanta tana share hawaye kewar mahaifiyarta tana sake bijirowa zuciyarta sosai tayi kuka Granny nata aikin rarrashinta cikin kukan tace “Ba damuwata yazo ba Granny damuwata shine son sanin yanda ya karɓi amanar da Mahaifiyata ta bar masa, meyesa ta amince na zauna da Aliyu tun kafin na amince dashi? Meyesa ta zaɓamin shi tace naje na zauna dashi harma take bani wasiyyar na zauna dashi iyakar wuya bayan shi tun yanzu ya fara juyamin baya Granny tunda na farka kwana uku kenan banga Daddyn Farooq ba kuma yanzu

naji kina faɗa cewar tunda aka kawoni asibitin nan washegari bai ƙara zuwa ba"

Sharce gumi Granny tayi ta kamo hannun Kharimatu da taketa zubar da hawaye tace “kinga Kharimatu inason ki cire komai a ranki don Allah ki manta da komai kinga cikinki ya tsufa watanni bakwai bakya buƙatar hayaniya ga kuma lalurar nan da take damunki don Allah ki daina sa Aliyu a ranki Kharimatu ba haka akabar Aliyu ba kinsani wannan lamari yana buƙatar addu'a me tsanani"
Jan zuciya tayi tace “Yanzu a haka zanta zama kenan?" Murmushi Granny tayi tace “Aa bazakiyita zama a haka ba yanzu abinma dake akwai zaki koma gabanmu ne aci aci gaba da magani har Allah ya baki lfyrki"
Zuciyarta na suya haka ta hƙr tabar mgnr ta koma ta kwanta kwana takwas ta ƙara a asibitin suka sallameta domin suma sun fahimci ciwon nata bana asibiti bane dole tasa aka nemi maganin Hausa tare da yin waya Guru aka sanar dasu halin da ake ciki Baba Na'ibi wane a gurin babanta shine ya niƙo gari ya taho Kano ya kawo mata magani cikin ikon Allah Suna fara amfani da maganin sauƙi yayita samuwa sati guda bata rufa ba wannan ƙanzo$^{2}$n da fatarta tayi duk ya ɓare asalin fatarta ta dawo Baba Na'ibi yana kallonta yayi murmushi yace “komai zai wucce da yardar Allah"

*Oum Hairan*
[11/10, 8:59 PM] Oum Hairan&Affan: *MYJ39-40 Oum Hairan* Littafina na kuɗi kada ki karanta min baki biya ba don Allah idan kinaso ki biya ta 0255526235 Gtbank ko ki turo hoton katin 300 ta wannan number 09013718241 saiki tura evidance of payment ta number dai ko VTU ta 0931307566

Kwanaki har watanni sukayita wuccewa babu Aliyu babu Salma Kharimatu tanata rainon cikinta har ya isa haihuwa ranar wata asabar da yamma ta shiga bayi tana tsugunnawa taga wani jini me yauƙi ya zubo mata ta miƙe da sauri ta fita ta kira Granny dake a sashinta take zaune. Tana gani ta gane meye ke faruwa tayi murmushi tace “Abin yazo Kharimatu haihuwa ce" gabanta ya faɗi tace “Granny tun jiya marata take ciwo fah" kama hannunta tayi tace “kije ki zauna bari nayiwa Mal Hassan mgn yayi miki rubutu idan haihuwar ce ciwon zai tashi ayi a wucce gurin idan ba ita bace kuma zaiyi sauƙi"
Zaunar da ita tayi ta shiga ɗaki bata jima ba ta fito ta tarar da ita ta riƙe ciki ta cije leɓe tana ƙoƙarin zamewa daga kujerar kamota tayi ta saukar da ita ƙasa tanayi mata sannu itadai kallonta kawai takeyi tana karɓar azaba babu jimawa Mal Hassan ya aiko da rubutun Granny ta

bata tasha tace ta kwanta, kwanciya tayi bacci ya ɗauketa cikin baccin taji azabar ciwon ta ƙaru ta zabura ta miƙe da sauri tana faɗin Innanillahi wa Innah Ilaihirraji'un Granny bayana marata ƙirjina wayyoh wayyoh Granny shikenan na mutu na ƙare...." Rufe mata baki tayi tace “ke ar sakarya ki rinƙa salati" fita Granny tayi tayima driven gdan mgn tazo ta ɗauko mata hijjab ɗinta tasa mata daidai lkcn Mom ta fito itama suka nufi asibiti suna zuwa aka shiga da ita labour room.

Bata wani ɓata lkc ba Ubangiji ya yassare mata ta haifo sankacecen ɗanta namiji kyakkyawa kamannin sa na mahaifinsa ne sak sumarsa da bakinsa sune kawai nata, ana gyara yaron aka sallamesu suka tafi gda sunata murna kamar ba'a taɓayi musu haihuwa ba.
Waya sukayi Guru ƙanwar Mama Yabi tazo ita da Granny suka rinƙa kula da ita abinda ya dami zuciyarta tun ranar data haihu take kiran wayar Aliyu bata shiga shikuma bai kirata ba zuciyarta na faɗa mata to ko baisan ta haihu bane?" Wannan abu sosai ya damu ranta ranar da ɗanta ya kwana biyar suna zaune take tambayar Granny Daddyn Farooq kuwa yasan ta haihu?"

Shiru Granny tayi tsayin lkc fuskarta ta sauya daga fara'a zuwa damuwa hakan ya tashi hankalin Kharimatu idanunta ya kawo ruwa tace “kiyi hƙr Granny bansan tambayar zata ɓata ranki haka ba insha Allahu bazan ƙara ba" riƙo hannunta Granny tayi ta share ƴar ƙwallar data zubo mata tace “ba tambayarki ce ta bata raina ba Kharimatu yanda kika damu da yaron nan Aliyu shi bai damu dake ba don Allah duk hukuncin dana yanke kada kiyimin gardama nasan kinason mijinki nima inasonki dashi zanyi ne don ƙwatar miki yancin ki"
Kallon ƙanwar Mama Yabi Granny tayi tace Saude idan anyi suna zaki tafi da Kharimatu Guru ta zauna acan duk abinda kuke buƙata zan rinƙa turo muku" amsawa Gwaggo Saude tayi da to sukaci gaba da tattaunawarsu itadai jinsu kawai takeyi tana kallon ɗan nata tana share hawayen tausayinsu daga ita harshi
Yaro kyakkyawa ya shigo rayuwar cikin yanayi mara daɗi rabonta da sanya mahaifinsa a idanunta tun cikinsa yanada wata biyu wannan wacce irin ƙaddara ce
Kwana nawa tayi na farin ciki da mijinta meye yasa ya gujeta ya daina bibiyarta.

Ranar suna yaro yaci sunan kakansa Ma'aruf akayi suna na mamaki kwanaki uku da sunan suka ɗauki hanyar Guru tunda ta koma Guru cikin danginta hankalinta ya kwanta damuwarta ta ragu gata ga ɗanta yanashan gata gurin yan'uwan mamansa Baba Na'ibi ne ya rinƙa kula da ita da duk wani motsinta kullum cikin yi mata rubutu da kawo mata magungunan tsari yake domin ya fahimci bayan rabata da mijin da akayi rayuwarta ma ake farauta don dai kawai tanada ƙarfin addu'a ne kuma ƙaddararta me ƙarfi ce.
Kullum zasuyi waya da Granny zataji abinda ke faruwa Mom ma tana kiranta taji lfyr jikanta duk watan duniya Abba yana tura mata kuɗi sosai shi a burinsa ma ta koma makaranta so ya

fahimci Aliyu yanzu bashida ra'ayin karatun mace hakan yasa ya tattara yabar batun karatun. Watansu takwas a Dubai suka dawo Ikcn Salma ta haifi yarta mace yarinyar tazo batada Ify ƙarshe ma ta mutu sosai sukaji mutuwar yarinyar tunda suka dawo zuciyarsa ta koma masa gurin Kharimatu musamman daya buɗe ɗakinta yaga batanan alama ma ta nuna itama ta daɗe rabonta da gdan.
Guri ya samu ya zauna daɓar zuciyarsa na bugawa da ƙarfi sai yanzu yake tuna a yanayin daya tafi ya barta da ƙaramin ciki wata uku gashi kusan watansa tara bayanan tsoro ne ya kamashi ya miƙe yace.

“To me hakan yake nufi Kharimatu nasan yanzu ta jima da haihuwa tun wata huɗu baya, me yasa ba'a faɗa masa ba? To kodai itama mutuwa abinda ta haifa yayi?" Da wannan tunanin ya lalubi numberta ya dannan kiran Ikcn tana islamiyyar dake gaban gdan nasu tana koyar da matan aure taji wayar tata tana ring ta zura hannu cikin doguwar rigar atamfar tata me aljihu ta zaro wayar tana kissing Jawad dake hannunta ta ɗora idanunta akan wayar da sauri cikin faɗuwar gaba tace “Aliyu Daddyn Farooq...." Wasu hawaye taji sun silalo mata ta kara wayar a kunnenta tare da yin sallama yaja wata ajiyar zuciya me ƙarfin gaske yace “Kharimatu kina inane Ina ɗana ko ƴata nasan zuwa yanzun kin haihu ko me kika haifamin?" Kallon ɗaliban nata tayi da suma suke kallonta kuka me ƙarfi ya kwace mata cikin tashin hankali ya fara kiran kinga Kharimatu kada ki ɗaga hankalinki faɗamin inda kike bari nazo ko kina gdansu Granny ganinan....."

*Oum Hairan*
[11/11, 7:50 PM] Oum Hairan&Affan: *MYJ41-42 Oum Hairan* Littafina na kuɗi kada ki karanta min baki biya ba don Allah idan kinaso ki biya ta 0255526235 Gtbank ko ki turo hoton katin 300 ta wannan number 09013718241 saiki tura evidance of payment ta number dai ko VTU ta 0931307566

Ƙit ta kashe wayarta ta juya ta fice daga ajin gabaɗaya ma ji tayi zaman makarantar yayi mata ƙunci wannan tasata barin makarantar ta shiga gda tana shiga Mama Saude ta tareta da cewa “meye kuma yake faruwa Kharimatu" bata iya bata amsa ba ta shige ɗaki ta kwantar da Jawad itama ta kwanta tanaci gaba da rera kukanta tanajin wayar nata ring taki ɗagawa.

Mama Saude ce ta ɗauki wayar ganin sunan dake jiki yasata jan tsaki tace “Aikin banza akan wannan sakaran mijin naki kike kuka to kiran me yake miki me zakiyi masa?" Ƙasa tayi da kanta tace “nima bansani ba ina makaranta ya kirani" tsaki ta kuma ja tace “Ki daina ɗaga wayarsa kwata² ki nuna masa kema kinada gata"
Kallonta tayi cikin yanayi na damuwa ta buɗe baki zatayi mgn sai kuma ta fasa har lkcn kiran wayarta yakeyi taƙ ɗagawa ƙarshe ma Mama Saude ta kashe wayar ranar hakanan ta yini sukuku babu ƙwari sai dare ta buɗe wayarta saƙonnninsa suka rinƙa shigowa ba ƙaƙƙautawa bata bata hankalinta wajen buɗewa ba ta gogesu taci gaba da harkokinta washegari da sassafe Mama Saude tace ta shirya zasuje Patiskum taso tayi gardama ganin Mama Saude ta dage yasata hƙr suka shirya suka bar Guru Gidan wata yayar Su Mama Yabi ne da Mama Saude a Patiskum.

Bayan sun huta ne Mama Saude take bawa Hajiya Bushira labarin abinda ke faruwa jinjina kai Hajiya Bushira tayi ta dubi Kharimatu tace “Kakar mijinki ta kawo shawara dole a cikin ido ake tsawurya duk da lamarinku akwai shiga tsakani amma shima yayi sakacin da sai an nuna masa kurensa zai gane yayi sakaci kiyi hƙr ki zauna anan har zuwa lkcn da tsohuwar nan zata buƙaci ki koma sonki takeyi shiyasa take miki gata" itadai batace komai ba domin ba gurin da zata ce ɗin bane tun farkonta tanajin tsoron masifar Hajiya Bushira shiyasa babu shaƙuwa tsakaninsu saboda bata zuwa gurinta
Da yamma Mama Saude ta tafi ta barsu sukaci gaba da zama a gdan Hajiya Bushira suna samun kulawa Hajiya Bushira akwai son yara ta kame Jawad ta goye kamar dama sun saba ltako hutawarta kawai takeyi tun tana ƙirga kwanaki harta koma ƙirga satittika tafi² har watanni biyar tama hƙr ta fawwalawa Allah ta cireshi a ranta yaronta yanata girma yana neman shekara mahaifinsa baitaɓa ganinsa ba.

Wata rana suka shirya domin zuwa duba Zahra ƙanwar Aliyu data haihu akayi mata aiki ita da Hajiya Bushira tunda suka shigo Kano gabanta ke faɗuwa suna zuwa gdan aka taresu da murna Umaimah ta ɗauke Jawad ta fice dashi sunata mamakin girman yaron da kamarsa da ubansa duk cikin yaran gdan babu me kama dashi kamar Jawad suna harabar gdan tanayi masa lilo motar Aliyu ta shigo tun daga nesa ya zubawa yaron idanu gabansa na faɗuwa dake tare take da sauran yaran suka fito idanunsa akan Jawad da keta dariya.
Yayi kamar ya wucce zuciyarsa taƙi aminta ya koma ya tsaya yana kallon yaron Umaimah ta ɗebeshi ta watsar dake dama ita ba jituwa sukeyi ba.
Bai damu da kallon da tayi masa ba yakai hannu zai ɗauki yaron daidai lkcn da Kharimatu ta fito daga parlourn tagansu tsaye yana ƙoƙarin ɗaukar mata yaro ta ɗaga murya da karfi tace “Karki bashi ɗana Umaimah!" Ba shiba hatta ita Umaiman saida ta juya bata damu da yanda ya kafeta da ido ba ta ƙarasa ta karɓi ɗanta a hannun Umaimah ta juya ta nufi sashin Granny.

Shikam Aliyu mutuwar tsaye yayi yana mamakin yanda yaron ya girma da irin muguwar canzawar da Kharimatunsa tayi cikin Ikcn daya ɗauka baiganta ba

Zama yayi a kan lilon ya kora yaran ciki yana tunanin to waishi me yaja masa wannan masifar ne yana son Kharimatu Amma ya yasa gane meye yasa ya kasa kataɓus don ganin ta dawo garesa gashi har ɗan su ya girma baitaɓa sanyashi a idanunsa ba wannan abin kunya da yawa yake shikam baiga laifinta ba data hanashi taɓa mata ɗa shi kansa yanajin kunyar kansa idan ya tuna yanada wani ɗan daya kasa basa  haƙƙinsa na ɗa kamar sauran ƴaƴansa.
Miƙewa yayi jiki a mace cikin rashin laka ya shiga sashin Granny suna zaune sun baje a parlourn sunata hirarsu da dariya Jawad nata haɗawa Granny shirgi tana masa tsiya babu wanda yasan dashi a tsaye saida Kharimatu ta ɗago idanunta ya faɗa cikin nasa tayi saurin kawar da kai tare da janyo Jawad ta matseshi a jikinta tasa masa nono yaron ya kama yana dukan jikinta ta lumshe idonta tare da miƙewa zatabar gurin ya kira sunanta da sauri.

Sai Ikcn Hajiya Bushira da Granny sukasan wainar da ake toyawa aikuwa Granny ta miƙe da sauri tace “Kai gantalalle Ify?" Sosai kalmar Granny ta dakeshi batajin kunyar aibatashi akan lamarin Kharimatu, cikin sanyi jiki yace “Am dama inason mgn da itane" harara ta zabga masa tace “wa kakeson mgn da ita Kharimatun? Kasanta ne meye alaƙarka da ita zaka ɓacemin da gani ko sai naci mutuncinka"
Tsayawa yayi zaiyi mata magiya ta ɗaga hannu ta ɗauke shi da mari tace “Aliyu bakaiba ko ubanka Ma'aruf bai isa nabashi umarni yaƙi biba Kharimatu ta dawo gdannan inasonta a kusa dani ba makaranta ma xansa Ma'aruf ya siya mata mota ta koma...." Da sauri yace

 “Makaranta kuma Granny da izinin wa?" Murmushi tayi tace “ai batada nauyin kowa a kanta aure ne nice dama nayi uwa nai makarbiya Yabi Allah ya jiƙsnta ta ɗauki marainiyar Allah ta baka dama saida Zahra tacemin Auren sha'awa kayi da Kharimatu naƙi yarda gashinan kuwa a hankali komai ya bayyana daka samu biyan buƙatarka saika banzatar da ita to mu munaso kuma Allah yanason kayarsa daga ita har Jawad ka cire su a lissafin ahalinka Kharimatu ta rayu a gdannan iya rayuwata idan na mutu ta koma danginta na haramta maka ita Aliyu har abada zan kira iyayenka su shaida"..........

*Oum Hairan*
[11/13, 12:33 PM] Oum Hairan&Affan: *MYJ43-44 Oum Hairan* Littafina na kuɗi kada ki karanta min baki biya ba don Allah idan kinaso ki biya ta 0255526235 Gtbank ko ki turo hoton katin 300 ta wannan number 09013718241 saiki tura evidance of payment ta number dai ko VTU ta 0931307566

Wani abu yaji ya caki ƙirjinsa ya ɗago da sauri yace “Haba Granny meye yasa kike wannan mgnr wlh tallahi ban auri Kharimatu domin cutar da itaba ke shaida ce inason Kharimatu Ni kaina bansan meye yasa na watsar da lamuranta ba" ƙasa yayi ya durƙushe yace “Granny kiyiwa girman Allah ki janye wannan furucin kinsani ina buƙatar iyalina a jikina Tunda Salma ta haihu batada Ify kina gani sai me aiki na ɗauka saboda yar....."
Ɗaga masa hannu tayi ta juya tace “Ka iya tafiya wannan kaita shafa ɗannan ba damuwar Hadizatu bace" kiranta ya rinƙayi taƙi sauraronsa ƙarshe ma ta shige ɗakin da Kharimatu take zaune.
Kanta na ƙasa tana kallon yanda Jawad ya kafeta da ido tana share hawaye lkc zuwa lkc a baya ta hƙr ta cire Aliyu a ranta meyasa yanzu data ganshi abubuwa suke neman jsgule mata meye yasa ko taga laifinsa wani sashi na zuciyarta yake wsnkesa da gaske ne kalamansa shi kansa baisan meye yasa yayi mata haka ba to amma meye yasa ya haɗa harda ɗanta shima an rabashi dashi kenan?

Lumshe idonta tayi Granny na kallonta itama Hajiya Bushira kallonta takeyi cike da tausayi itakam ƴartata tana bata tausayi abubuwa sunyi mata yawa ga maraici ga rashin miji damuwa dole ta samu matsuguni a rayuwarta.
Muryar Granny ta tsinkayo tana cewa kada ki sake ki sawa kanki damuwa akan Aliyu Kharimatu inada tabbacin Allah zaiyi miki sauyi mafi alkhairi tabbas Allah baya wulaƙanta marayansa da yardar Allah duk wanda yake da hannu wajen rabaki da mijinki shima sai Ubangiji ya hanashi jin daɗin tasa rayuwar" kuka ne ya ƙwace mata ta riƙo hannun Granny tace “Wlh inason cireshi a raina na kasa Granny ki tayani da addu'a" shafa kanta tayi tace “mijinki na fari uban ɗanki ai bazai taɓa ciruwa a ranki ba saidai ki koyi dakiya da shariya Kharimatu naji daɗin abinda kikayi masa ko banza ya fahimci kinsan ciwon kanki kema kuma zuciyace a jikinki"
Sunata hirarsu da Granny da Hajiya Bushira itadai kawai kallonsu takeyi tana jan zuciya sai

Magrib suka tashi sukayi sallah ta kama hannun Jawad suka fito suka nufi cikin gdan yanata yi mata gwarancinsa tana biye masa. Da sallama suka shiga Mom na parlourn tana ganinsu tayi murmushi tana satar kallon Aliyu dake kwance tun ɗazu tunaninta ma bacci yakeyi sai yanzun da taga ya buɗe idonsa akan Kharimatun tace "Au dama ba bacci kakeba kanaji ana sallah"

Tashi yayi zaune yana kallon Jawad da ya saki Maman tashi ya nufi kakarsa da tafiyarsa da batayi ƙwari ba tararsa Mom tayi ta ɗagashi ta cafe tace "Wato girmanka Jawad yana bani mamaki saikace ana buga maka iska" murmushi Kharimatu tayi tace "Haka kowa yake cewa yayi saurin girma nikam bana ganin girman nasa" dariya Mom tayi tace "Haba Kharimatu shekara ɗaya yaro kamar ya shekara biyu yaushe zaki yayeshi?" Ƙasa tayi da kanta tana murmushi tace "Waida yayi wata ashirin ko ya kika gani?" Jinjina kai tayi tace "Hakanma yayi amma ki cireshi da yayi sha huɗu saboda kinga makaranta zaki koma ga form ɗinki canma Dad ya siyo miki registration káwai zaiyi miki da ɗan abinda ba'a rasa ba saidai makarantar ba anan Kano take ba Alkalam University dake Katsina ya sama miki zaman hostel ya ganki shikuma karatu bazai yiwu da yaro ba"

Miƙewa yayi ya ɗauki wayarsa da key ɗinsa ya fice daga ɗakin babu jimawa daya cikin masu aikin gdan ya dawo ya dubeta yace "Yallaɓai ke nemanki a waje" ɗagowa tayi suka haɗa ido da Mom diririce tace "am in kaje ina zuwa" murmushi tayi tace "tashi kije ya ɗauke miki ɗa kinsan bayason jira zai iya tafiya dashi"
Miƙewa tayi ta fito yana tsaye jikin motarsa sarai tagansa ta kawar dakai tayi wuccewarta Jawad yana ganin ta wucce ya rushe da kuka yana kiran Aunty tanaji Aliyu na ƙwala mata kira taƙi ko tsayawa bare yasaran zata waiwayo ganin haka yasashi binta da sauri dake itan ba sauri takeyi ba baisha wuyar cimmata ba yasha gabanta saura ƙiris ta shige jikinsa tayi baya da sauri yaja numfashi yace "Wai meye ke faruwa ne Kharimatu na zaci idan kowa ya juyamin baya ke zaki kalleni ta gaba" ɗagowa tayi ta kafesa da manyan idanunta ya janye nasa daga cikin nata sosai idanunta keyi masa kwarjini baya jurewa kallon ƙwayar idonta baki ta buɗe cikin sanyin muryarta tace
"Matsa zan wucce" baice mata komai ba kuma bai matsa ba ta canza hanya ya riƙota yace

"Ki fahimceni Kharimatu wlh ba laifina bane bansan matsalar da haɗaku gda ɗaya da Salma zata haifar kenan ba da wlh bazan haɗaku ba kinaji ba kinsani Baba Na'ibi ne yazo bama na ƙasar nan lkcn aka buɗe masa gdana ya shiga suka ƙwaƙule binne binnen da akayi a ɗakinki da ƙofar shiga gdan ko shekaran jiya munyi waya dashi ina faɗa masa matsalata inasonki inason

dawo dake cikin rayuwata amma na kasa takawa naje inda kike idan na kiraki baki ɗagawa cemin yayi na jirashi minti biyar babu jimawa ya kirani yace naje ɗakina cikin wardrope ɗina ta tsakiya cikin kayana na birkita sosai akwai wata laya nayi bismilla na ɗauketa na warware na zuba mata fitsari ko ruwan kwata na ƙona ta wannan itane abinda ya raba tsakanina dake. Kharimatu
nayi yanda yace ɗin kuma tun ranar na samu relief ya kasance kullum cikin tunaninki nake Kharimatu ki tambayi Mama Saude cikin kwanaki ukun zuwana Guru biyu tana cemin bakyanan na tambayeta inda kike taƙi faɗa min na dawo na tambayi Granny ta ci mutuncina Dad har marina yayi akanki Mom ce kawai take tausayina cikin lamarinki"

Murmushi tayi me ciwo tace “Naji bani hanya na wucce" yanda tayi mgnr yasashi kallonta yace “Baki yarda ba ko Kharimatu?" Ɗagowa tayi ta kalleshi tayi masa murmushin daya sanyashi sakin baki yana kallonta tace “Ina tunanin saboda ɗanka daka banzatar ka watsar da rayuwarsa ya kasance da mutuwarsa da rayuwarsa duk basa cikin abinda ya dameka kake bibiyata ko? Ok Indai saboda Jawad ne gashinan ka riƙe abinka don Allah ka rabu da rayuwata Aliyu inason Jawad amma na hƙr nabar maka abinka nasani tunda Allah ya azurtani da cikin haihuwa idan Ya nufeni da sake aure zan haifi madadinsa....."
Wata tsawa ya buga mata yana huci jikinsa na rawa yace “Ni kike faɗawa zakiyi aure ki haifi wasu yaran kuma da igiyoyin aurena uku akanki saboda bakida mutumci" bata tsaya sauraronsa ba ta juya tayi tafiyarta tanaji yana kiranta bata juyo ba saima sauri data ƙara ta shige sashin Granny ta datso ƙofar ya iso da sauri ganin yanda Jawad ya ƙara rushewa da kuka.

Granny ce ta fito saboda kukan da ta jiyo Jawad yanayi turus taja ta tsaya ganin Kharimatun zaune a falon tana share hawaye, matsawa tayi gareta ta dafa kafaɗarta tace “Ina kika baro Jawad ɗin nake jiyo kukansa?" Ƙasa tayi da idanunta tace “Ya....yana gurin Babansa" bata kuma ce mata komai ba ta nufi ƙofar ta buɗe ta ishe Aliyu sai rarrashin yaron yakeyi yaƙiyin shiru.
Yana ganinta ya fara miƙa mata hannu ta dubi Aliyu da duk ya ruɗe duk da darene hasken dake gurin ya bata damar ganin yanda idanunsa ya kaɗa yayi jawur tayi juyawarta zatayi tafiyarta ya riƙota yace “kiyiwa Allah kada ku hukuntani da haka kuka yakeyi Granny kuma nono yakesha idan ita batada hankali ta tafi ta barni dashi aike babbace kinsan daidai" fusge hannunta tayi tace “Irin hankalinmu ɗaya Aliyu itama tana buƙatar hutu tunda ba ita kaɗai tayi cikin ba hasali ma kafita ƙarfi lkcn da za'a samu cikinsa domin gashinan ya bayyana kansa duk wanda yagansa yaganka yasan jininka ne kaje ka haɗashi da ƴan'uwansa"
Zuba mata ido yayi kukan yaron yana masa kuɗa a kunne ya juya zuciyarsa na zafi idanunsa sai raɗaɗi sukeyi ya isa motarsa ya buɗe ya shiga har lkcn Jawad kuka yakeyi ɗagashi yayi ya

rungumeshi a ƙirjinsa yaron ya ƙanƙameshi yayi luf a ƙirjinsa yana sauke ajiyar zuciya, so ƙauna da tausayin ɗan nasa yaji yana ratsa jinin jikinsa yanda yaron yayi luf a ƙirjinsa yasa hawaye zubo masa wato shima yana buƙatar duminsa, meye yasa ya nesanta kansa dashi?"

*Oum Hairan*
[11/14, 8:41 PM] Oum Hairan&Affan: *MYJ45-46 Oum Hairan* Littafina na kuɗi kada ki karanta min baki biya ba don Allah idan kinaso ki biya ta 0255526235 Gtbank ko ki turo hoton katin 300 ta wannan number 09013718241 saiki tura evidance of payment ta number dai ko VTU ta 0931307566

Kasa tashin motar yayi yaci gaba da jijjiga yaron har saida yaji numfashinsa ya sauya ya saukeshi yaga ashe yayi bacci yaja fasali ya kwantar dashi a kujera yaja motar ya fice a gdan zuciyarsa a hassale ya nufi gdansa yayi parking ya fito ya ɗauki Jawad ya kulle motar ya nufi cikin gdan buɗe ƙofar yayi ya shiga dake shi ɗaya ne a gdan ya kwantar da yaron a gadonsa ya zauna ya haɗe kai da gwiwa yanajin zuciyarsa na tafashi lkc zuwa lkc yana furzar da iska me zafi bashi ya kwanta ba sai wajen 1:30am bawai bacci ya kwanta yayi ba tunanin mafitarsa kawai yakeyi.
Bayan tafiyarsa Granny ta koma ɗakin da Kharimatu take ta dubeta tace “meye yasa kika bari ya ɗauki yaron nan?" Ɗago idanunta da suka jima da jiƙewa da ruwan hawaye tayi tace “bansan ya ɗauke shi ba Granny Jawad ya fita wajen parlourn Mom yana wasa anan ya ɗaukeshi" jinjina kai tayi Hajiya Bushira tace “Yanzu ina Jawad ɗin?" Granny ce tace “cewa nayi ya tafi da abinsa itama ta huta...." Zaro ido Hajiya Bushira tayi tace “Ya tafi dashi kuma Hajiya amma kunyi ganganci yanzu idan matar nan da ba ƙaunar Kharimatu take ba ta huce haushinta akan Jawad fah" Murmushi Granny tayi tace “Nasan Halin Aliyu koda Salma nanan bazai taɓa yarda ta taɓa masa ɗa ba balle Bama tanan tana gdansu tana jinya tunda ta haihu ta haɗu da lalura Cancer mahaifa ce ta kamata sai kuma irin ƙurajen da kikayi da cikin Jawad sunanan sun feso mata sai mugunya take zubarwa sunje asibitin sunyi na gargajiyar ance dasu ƙaiƙayi koma kan masheƙiya akayi mata ita tayiwa kishiyarta shine Abin ya dawo kanta"

Zuciyar musulmi sai Kharimatu taji tausayin Salma ya ɗarsu a ranta tace Allah sarki Granny na tausaya mata ciwon nan akwai wahala ubangiji ya bata lfy" taɓe baki Granny tayi tace “karma ta samu lfyr mugun nufinta ne ya koma mata nifa dama bantaɓa ƙaunar yarinyar nan ba wlh bata kwanta min ba shima donta zame masa jaraba ne"
Itadai Kharimatu tunanin ɗanta kawai takeyi ta kwanta ta juya musu baya sai hawaye take

sharewa tana tunanin yanda zai kwana babu ita   daƙyar bacci ɓarawo ya saceta shima bana daɗi ba da safe ma data tashi duk wani sukuku ta tashi ga nononta ya cika sai damunta yakeyi basarwa kawai takeyi tana duba agogo lkc zuwa lkc kawai so take taji zuwan Aliyu amma shiru har la'asar.

Sai bayan Magrib ya shigo gdan yayi parking tana tsaye jikin window ta zuba masa ido tana ƙare masa kallo cikin hasken daya mamaye gurin sai yanzu take ganin ramar da akace yayi Granny ta Bata Ibrn wata tunda suka dawo Salma ta tafi gdansu yaran nasa a gurinsa suke shine komansu Salman da kanta tace bazaa ɗorawa iyayenta wahala ba sosai taji tanajin tausayinsa duk aikin da akace ba naka bane idan aka Barka dashi an jarabci rayuwarka, ganin ya saɓa Jawad a kafaɗarshi taji kamar taje ta kwace ɗanta tana ganinsu suka shiga sashin Mom ta zari mayafinta tayi waje itama ta nufi sashin Mom ɗin tana kai kanta zata shiga shikuma yana fitowa ganintan da yayi yasashi cafkar hannunta da ƙarfin da bata isa ta ƙwace ba ya nufi motarsa da ita suka tsaya jikin motar ya ja numfashi ya ɗago idanunsa akanta yace “Wlh duk girman laifina gareki ban cancanci wannan horon ba Wlh Allah ɗaya Kharimatu da rana ɗaya bantaɓa rabuwa da tunaninki ba don Allah kiyi hƙr ki manta da duk abinda ya faru nayi miki alƙawarin bazai sake faruwa ba har abada insha Allahu"

Zame hannunta tayi ta juya tabar gurin yabita da kallo yana mamakin kafiyar yarinyar a fili yace “dama haka kike?" Tambayar kansa yayi bashida amsa haka ya shiga mota ya tafi ta shiga sashin Mom tana shiga Jawad ya taso da gudu har yana faɗuwa yana fasa baki amma bai fasa isowa gareta ba ta kalli Mom so take ta ɗaukeshi kunyar Mom ta hanata murmushi Mom tayi tace “ki ɗauki ɗanki Kharimatu banda shashancinki meye na barinsa ya tafar miki da ɗa" ajiyar zuciya tayi tasa hannu ta ɗaukesa ta rungumeshi ya ƙanƙameta shima hawaye ya zubo mata tayi saurin sharewa ta zauna suka gaisa da Mom suka taɓa hirarsu Mom tace mata “Kharimatu nafi yi miki sha'awar komawa gdan mijinki fiye da zaman nan da kikeyi Aliyu yana sonki Kharimatu wlh na tabbata bayin kansa bane abubuwan da suka faru da farko naji haushinsa sai daga baya na fahimci sharrin mace ne yasashi aikata duk abinda ya aikata kiyi hƙr badon Aliyu ba domin Allah ki komawa Aliyu kinji?"

Tunda Mom ta fara mgnr take matsar idanu harta gama ta zuba mata idanu tanason taji cewarta, ƙasa tayi da kanta tana wasa da ƙafar  Jawad da yaketa ɓaɓɓaka dariyarsa mom ta sake magantuwa da cewa “bakice komai ba Kharimatu ko bakyason zamanku da Aliyun ne?" Hawayen ta share tace “Ba haka bane Mom kawai inajin tsoron kada tarihi ya maimaita kansa

Mom banida uwa banida uba banida ɗan'uwa shakiƙi da zanyi magana dashi naji daɗi idan na rasa gatan miji to rayuwata batada wani amfani domin zanyita da ƙunci ƙuncin da zaike azabtar da ruhina Wlh Mom Inason mijina Amma inajin tsoron abinda ya faru ya kuma faruwa" murmushi Mom tayi tace "Indai kinason mijinki to kuwa zaki koma ɗakinki Kharimatu itafa wacce kike wannan abin akanta ma yanzu ba matarsa bace ita da kanta tace saiya saketa wai asiri kikeyi mata akansa mukuma bincikenmu ya nuna mana itace tayi abinta ya koma mata itama mahaifar tata data taɓu taketa zubar da jini ba ciwo ne na Allah da Annabi ba ke akaso ɗorawa abinta ya dawo kanta amma ta kwarzabi kanta shine fa yayarta ta kirashi Suka ƙare masa tanadi kinsanshi shikuma babu hƙr aikuwa a ranar ya raba kansa da ita ta rigashi dawowa ma daga tafiyar da sukayi ashe ita tafi wata biyu a ƙasar nan shine da yaran acan koda suka dawo ma bai sanar damu basa tare ba sai jiya daya kawomin yaran"

Cike da tsoro tace "Mom basa tare fah kikace" jinjina mata kai tayi alamun tabbatarwa tace "harma ta kusan gama idda zanyima Alh mgn yayima Granny magana tayi hƙr ta baku dama ku gina rayuwar ku kinji" Kharimatu dai shiru tayi tana tunano irin mulkin da Salma ta shimfiɗa a gdannan wai yau batanan lallai rayuwa babu tabbas dole kabita a sannu.
Wayarta ce taji tana ring ta zarota ganin sunansa yasata kifa wayar tare da sata a silent yayi kira yafi nawa taƙi ɗagawa shigowa yayi parlourn ya cika da mamaki ganinta zaune arziƙin ɗaga wayar tasa ne babu ya jinjina kai kawai ya fice, bata wani damu ba taci gaba da zamanta saida taji tashin motarsa sannan ta miƙe ta nufi sashin Granny bata gama zama ba Granny tace "Yanzu mijinki ya fita nikam ya sanyaya min jiki harma nayi karambanin cewa dashi yaje nanda sati biyu zaki koma gdanki amma da sharaɗin koda zai dawo da matarsa bazai haɗaku gda guda ba sannan zai barki kiyi karatunki kuma duk ya amince harma yace cikin satinnan zai siya miki mota".......

*Oum Hairan*
[11/17, 9:16 AM] Oum Hairan&Affan: *MYJ47-48 Oum Hairan* Littafina na kuɗi kada ki karanta min baki biya ba don Allah idan kinaso ki biya ta 0255526235 Gtbank ko ki turo hoton katin 300 ta wannan number 09013718241 saiki tura evidance of payment ta number dai ko VTU ta 0931307566

Shiru tayi tana tariyo irin abubuwan da suka faru a baya zuciyarta na ayyana mata idan ta koma fah waɗanda suka fisu zasu iya faruwa ita kanta ta shaida tanason Aliyu saidai tana tsoron rayuwa da asiri komai addu'arka wataran saiya taɓaka tunda ya taɓa ma'aikin Allah hawaye taji

ya zubo mata Hajiya Bushira ta sanya hannu ta share mata tace “Haba Kharimatu ai da canma sakaci akayi yanzu kuwa tunda komai ya bayyana ai kije ki rayu gidan mijinki da zuciya ɗaya ki ƙaddara fah komai ya wuce" jinjina kai Granny tayi tace to mema zai faru ai insha Allahu Salma tabar Aliyu kenan har abada"
Kasa furta komai tayi saidai kawai ajiyar zuciya da take

Shawarwari Hajiya Bushira ta jata ta rinƙa bata duk jikinta ya mutu da dare suka kwanta washegari da wuri suka shirya tafiya Patiskum ɗin suna tsaka da shiri ya shigo suka gaisa da su Granny Itako ko kallonsa batayi ba ta miƙe ta shige ɗaki ya jinjina kai ya juya ya fita batare da yace komai ba Granny ce ta shiga ɗakin ta sameta tace “Mijinki yace “Tare zakuje kukai Hajiya Bushira ku dawo da sauri ta ɗago idanunta tace “Mu dawo kuma Granny?" Jinjina kai tayi tace “Eh ki biyosa ku dawo" shiru tayi amma hukuncin yayi mata tsauri sosai batason takura a rayuwarta.
Fita akayi da kayan akasa a Motar suka fita suka shiga yaja suka tafi yanata jan Jawad da wasa itadai ta gimtse ko uhm bata cewa sai bin hanya kawai da takeyi da kallo Ikc zuwa Ikc tana share hawaye tunda suka taho ya lura da sharar hawayen da takeyi baidai ce mata komai ba zaman kurame akayi har sukaje Patiskum idan anyi mgn a motar to shida Hajiya Bushira ne ko kuma yana yima Jawad wasa suna zuwa ta fita a motar ta shiga gda ta shige ɗakinta sai yanzu ta samu damar yin kuka isasshe ganin rayuwarta takeyi matsayin ƙararrriya wahalar da tasha ta kasa goge mata Allah ya sani badon girma da mutumcin Iyayen Aliyu a gurinta ba da ko zata mutu saboda sonshi bazata sake yarda ta zauna zaman aure dashi ba saidai kash sunfi ƙarfin komai a gurinta dole haka zata zauna dashi tayi hƙr da ƙaddararta

Basu wani jima ba abinci kawai sukaci wajan la"asar yace su fito su tafi Hajiya Bushira dakanta ta rinƙa shirya mata kayanta tare da bata wasu tarkacen mata masu yawa ta rubuta mata yanda zatayi amfani da kowanne ya ɗaukesu suka tafi tunda suka taho Ikc zuwa Ikc yake kallonta Lkcn da suka shigo Kano ana sallar Isha ya dubeta ya kawar dakai tare da juya kan motarsa zuwa Nassarawa G.R.A ya nufi wani babban gurin saukar baƙi saida yayi parking ta fahimci inda ya kawosu gabanta ya faɗi ta ɗago da sauri tace “Ya haka?" Murmushi kawai yayi mata ya fita tana ƙoƙarin fita ya kulle motar ta zauna ita ɗaya don ya ɗauke ɗansa basu jima ba suka fito ya buɗe mata motar ta fito fuskarsa babu wasa yace mata "muje" babu musu tabisa suka shiga ya buɗe dakin daya kama musu ta maƙale a ƙofa ya shiga ya kwantar da Jawad dake bacci ya tako ya iso gabanta ya riƙo hannunta ya janyota ciki ya kulle ƙofar matsawa tayi daga kusa dashi ya shafa gemunsa yace “Ina mamakin yanda kike son azabtar dani da wata sabuwar ɗabi'a Kharimatu kiyi hƙr badon niba domin Allah babu abu ɗaya da nayi miki don raina yanaso Kharimatu anayin tafi haka ma kuma a dawo a zauna so don Allah ki manta da komai muyi rayuwa me inganci"

Ɗagowa tayi ta zubansa idanu can ta kautar dakai tace “Naji ka bani dama na tafi gda banason hotel ɗin nan daka kawoni idan ka matsa zan ƙara yarda a raina har yanzu banida yanci banida galihun da za'a saurari cewa ta sannan....." Rufe mata baki yayi yace “Ba haka bane Kharimatu taimakona zakiyi don Allah kada ki gaza nasan keɗin me tausayi ce" tubure masa tayi ta zauna ta sashi a gaba ta rinƙa kuka iyakar kalamansa saida suka ƙare gashi bazai iya jure kukanta ba hakan yashi miƙewa ya ɗauki Jawad yace “Shikenan muje Kharimatu" miƙewa tayi da sauri ya buɗe mata ɗakin ta fice suka shiga wamota yanata huci zuciyarsa nayi masa zafi ya rasa yaushe Kharimatu ta koyo kafiya da taurin kai.

Yanayin parking bai gama tsayawa ba ta fice daga motar yabita da kallo tare da murmushi ya fita yabi bayanta suka gaisa da Granny tayi musu Barka da dawowa sannan yayi musu sallama ya tafi.
Yana fita ta faɗa wanka ta haye gado ta kwanta sukaci gaba da hirarsu da Granny har bacci ya ɗauke su. Cikin kwanakin da suka rage mata na komawarta gdan mijinta tasha gyara ba kaɗan ba tare da karɓar mata magungunan tsarin jiki takanas Babanta Mal Wada Na'ibi yazo ya sake kawo mata magungunan tsarin jiki ta kuwa duƙufa yi takeyi sosai yanda ta bashi amanna ko magungunan matan bata basu haka ba,
Yanda Aliyu keta rawar ƙafa yana bata mamaki kuɗi yake kashe mata bana wasa ba duk abinda Granny ta kirashi tace kawo miƙawa yakeyi ranar juma'a ta kama zata tare itadai yinin ranar yinsa tayi jikinta duk babu ƙwari da magrib yazo gdan tana kwance a ɗaki Dad ya Kira wayarta ta ɗaga suka gaisa da ladabi yace taje yanason ganinta.

Tashi tayi ta yafa mayafinta ta fito ta nufi sashin Mom tana falon suka gaisa ta shiga ciki gabanta ya faɗi ganin Aliyun zaune a parlourn ta nemi guri ta zauna suka ƙara gaisawa da Dad yayi gyaran murya yayi musu nasiha me shiga jiki dukkansu saida jikinsu yayi sanyi yayi musu fatan alkhairi yace “idan ƙura ta lafa Aliyu nasa a canza mata admission daga Alƙalam zuwa B.U.K so amma samu angama registration da komai fara zuwa ne kawai nata am ga motar dana siya mata can a rufe d tampol a waje Kharimatu sai a mayar da hankali ayi karatu don Allah kada asa wasa"
Jinjina kai tayi tace “Insha Allahu Dad na gde ubangiji ya ƙara girma da Arziƙi Allah ya rabaka da Granny Ify" amsawa sukayi da Amin suka tashi suka tafi ya buɗe mata mota sai wani baje baki yakeyi yaja suka tafi saida sukaje gdan ta gane ashe sabon gdan daya gina zaisata farkon

aurensu ne da ba'a bari yasata ba taja numfashi yayi parking suka shiga ciki suna shiga ya ajiye Jawad ya janyota jikinsa ya rungumeta ya sauke ajiyar zuciya yace “Allah shine mafi soyuwa daa godewa Allah na gde maka daka sake dawomin da Kharimatu na cikin rayuwa ta"

Yanda ya rinƙa lallabata ya tabbatar mata yau saidai ƙwacen Ubangiji ne zai fitar da ita aikuwa hakance ta faru bayan sunci sunsha komai ya lafa suka shiga domin kwanciya ta kwantar da Jawad ta cire kayanta tasa na bacci ta haye gado ta ja bargo tare da rungumeta ɗanta yana kallonta baice mata ƙala ba yaci gaba da danne²nsa a system ɗinsa bayan ya gama ne ya tashi ya shiga bayi yayi wanka ya ɗauro alwala ya dawo ya haura gadon ya janye Jawad yamai dashi gadonsa ya shige gurin daya ɗauke yaron ya fara shafa fuskarta zuwa ƙirjinta tana jinsa ta shareshi kamar bataji ya rinƙa sarrafata yana wasa da ita dole saida ya kamata a hannu wannan dare Aliyu ya kwashi gara itakuma taci wuya lkcn da zaiyi release yanda ya ƙanƙameta kamar zai tsaga jikinta ya shiga sun jima a haka sannan ya janye jikinsa ya koma gefe.
Dole ce tasa ta saki jikinta dashi suka ɗora rayuwarsu fiye ma data baya satinta uku da dawowa gdan ta kama zazzaɓi me zafin gaske duk dauriyarta saida suka dangana da asibiti aka bincikata sosai suka tabbatar musu shigar ciki ke gareta wata runguma da Aliyu yayi mata saida ya bata tsoro  ta ƙanƙameshi yayi kissing nata yace “Wlh ranar da muka fara haɗuwa cikin nan ya shiga Kharimatu naji yanayina dama ya bani hakan zata iya faruwa ubangiji ya raya mana ya inganta"

*Oum Hairan*
[11/17, 10:33 PM] Oum Hairan&Affan: *MYJ49-50 Oum Hairan* Littafina na kuɗi kada ki karanta min baki biya ba don Allah idan kinaso ki biya ta 0255526235 Gtbank ko ki turo hoton katin 300 ta wannan number 09013718241 saiki tura evidance of payment ta number dai ko VTU ta 0931307566

Lumshe idanunta tayi yajata ya zaunar da ita likitan ya rubuta mata magunguna ya fita ya siyo ya dawo suka tafi kwanaki kaɗan komanta na makaranta ya kammala da farko Aliyu so yayi ya hana wai sai ta haihu Dad yace kada ya soma yabarta tayi karatunta dole haka ya barta amma ya hanata jan mota saidai ya kaita idan lkcn tashinta yayi yaje ya ɗaukota cikin watannin koma ya saitu ta sanyashi ya ɗebo mata yaran duka ta haɗasu su huɗu a gabanta ta riƙe dama dake sun saba da ita basu wani samu matsala da ita ba sukaci gaba da rayuwarsu kamar baya.
Sannu² lkc yayita shuɗewa har ubangiji ya nufeta da haihuwar yaranta biyu duka maza aikam yaran sunga gata bayan suna da sati ɗaya da safe suna falon suna hirarsu dake ranar ta kama asabar ce Aliyu yana gda yaran ma dukkan sunan knowking na ƙofa akayi ta miƙe ta buɗe gabanta ya yanke ya faɗi cikin firgici tace “Aunty Salma!" Dukka har yaran suka ɗago suna

kallon me shigowar ta ƙara so a duke kamar tsohuwa ta zube a tsakiyar falon.

Wani wari ya dumame gurin yaran suka tashi da sauri suka gudu Farooq yana cewa “Aunty mu mun gudu bamason ganin dodon nan Jawad zo mu gudu Aunty ki bani twins mu tafi sama dasu" hawaye Salma ta share cikin kuka tace “Me yajamin banda nadama nayi jayayya da hukuncin ubangiji Yaya Ameey ta ɗorani a muguwar hanya gashi nice na kwana ciki inason mijina tasani na rabu dashi na rabu da ƴaƴana Kharimatu duk akanki baƙin kishina yajamin na nayi muku asiri akan idan kun tafi hanyar zuwa Guru Ikcn bikinku kuyi hatsari ku mu dake ƙaddararki bata mutuwa bace kika tsallake saidai haƙƙin ran mahaifiyarki daya rataya akaina babu wanda yasan wannan haka nayi amfani da damar na yaudari mijinki ya amince zai haɗamu gda ɗaya da nasa aka turo manyan shedanu da zasu illataki daƙyar suka samu damar shafsrki suka zuba miki firgici wannan bai isaba nasa aka turo miki lalura sannan nasa a kashe ɗan cikinki bansan ya akayi ba duk abubuwan dana ƙulla suka dawo kaina na juyar da hankalin mijinki na janyeshi munbar ƙasar a Ikcn da bakida Ify ashe kaina nayiwa memakon ɗan cikinki ya mutu tawa ce ta mutu nasa a lalata miki mahaifa kiyita zubar da jini idan kin samu ciki kiyita ɓarinsa ashe kaina zata juyo shekara biyu kenan bantaɓa hutawa da zubar jini ba kullum cikin ƙaramin jini ake.
Gashi waɗannan ƙurajen dana sa a turo miki sun dawo jikina kullum cikin ɗoyi nake da zubar da mugunya gashi duk me maganin da naje gurinsa cemin yake kin samu kariya daga Ubangiji babu kuma wanda zai bani maganin ciwon nan nawa sai Babanki Mal Wada Na'ibi jiya mukaje gurinsa yace sharaɗin shine nazo na sanar dake nice nayi miki komai idan kika yafemin zai bani magani idan baki yafeba kuma saidai na zauna da ciwo na don Allah na roƙeki ki yafemin Kharimatu ina cikin mawuyacin hali....."

Ta karashe mgnr da wani kuka me gunji Tsaki Aliyu yayi ya miƙe yace da Kharimatu ta tashi tabar gurin kallonsa tayi da idanunta da itama suketa zubar da ruwa tace “Duk da inajin ciwon kasancewarta silar gushewar rayuwar Mahaifiyata bangona Yaya Aliyu bazan kasa yafe mata ba kodon arziƙin su Farooq da Muwaddat da Jannat kije Allah ya baki Ify Ni na yafe miki haƙƙin rai kuma banida ikon yafeshi tsakaninki da ubangijinki ne" miƙewa tayi tabar gurin da sauri don Allah ya sani batason ganin Salma.
Duk da halin da Salma take ciki miƙewa tayi tana ƙwafa a ranta tana cewa zakuyi bayani ne kudai jira naje na samu wancan tsohon banzan ya bani magani na warke wanda zanyi muku gaba ma sai yafi wannan saikin haukace kin fita tsirara mota ta takeki tunda kika zamo silar rabuwata da mijina sannan kika rabani da ƴaƴana"

Daƙyar Aliyu ya rarrashi Kharimatu ta manta da komai sati biyu tsakani suka samu kira daga gun Mom take sanar dasu sunji Ibrn mutuwar Salma kuwa sosai Kharimatu ta shiga cikin tashin hankali tace wlh batasani ba nan Mom tace mata ai sunje Guru sun dawo ambata magani taji sauƙi suka ɗauki hanyar Maiduguri gurin wani sabon bokansu so kafin sujene sukayi hatsari mutum biyu ne suka fita ciki harda ƙawar Salma wacce tayi mata jagora zuwa gurin bokan" Mutuwar ta bugesu sosai Kharimatu taji tausayin su Farooq ƙaunarsu ta ƙara shiga ranta duk da Aliyu yaso hanata zuwa ta'aziyyar tace masa yayi hƙr yabarta suje da yaran  hakanan ya ƙyalesu suka tafi harshi sukayi ta'aziyyar suka dawo, Kharimatu ta sake ɗaukar ɗambar riƙe yaran sukaci gaba da rayuwarsu kai zaka zacima duka ita ta haifa cikin ikon Allah bata yaye twins ba ta kuma haihuwar ƴa mace taci sunan Mahaifiyarta Ruƙayyatu sukece mata Amnah bayan shekara biyu ta ƙara haihuwar namiji shikenan haihuwar ta tsaya dake ita dama ahlinsu ba masu haihuwar da yawa bane.

Ta gama karatunta a fannin Business and Administration dake Allah yayita da son ƙamshi hakanan takeyin turaruka matan lay-out ɗin nasu suna siya ganin hakan batare data sani ba Aliyu ya siya mata wani babban shago ya zuba mata kayan kwalliya tare da kayan gyaran gashi da kuma ɓangaren boutique da turaruka humra kulacca turarukan wuta da kuma turaruka ƴan waje cikin Ikc ƙanƙani Ubangiji ya sawa Kharry Boutique and cosmetic albarka ya haɓaka ko ina zancen sa akeyi a yankin arear tasu haka ta kuma buɗe wani shima ya samu karɓuwa ga ƴaƴanta biyar dana mijinta uku yaransu takwas ta haɗa ta riƙe rayuwa tayi daɗi tayi riba albarka ta sauka ta wanzu a wannan zuri'a

_Tammat bi hamdullah_

_Alhmdllh gdy ta tabbata ga Ubangijin talikai daya bani ikon kammala wannan littafi a yau ɗin nan ina roƙon Allah daidanmu ya karɓa akasinta ya share ubangiji yasa ya amfanar_

Sanarwa! Sanarwa!! Sanarwa!!!

Insha Allahu sabon littafi na me suna BAƘIN RUHI zai fara zuwar muku 20/11/2021

*Oum Hairan*